MU KOYI IBADA

Sa'idu Muhammad Gusau

Century Research and Publishing Limited
Kano-Nigeria

Century Research and Publishing Limited
Abuja Kano Kaduna Lagos Zaria

© Sa'idu Muhammad Gusau, 2014
Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya,
Jami'ar Bayero, Kano

ISBN – 978- 978- 48643- 6- 7

An gama shiryawa a watan Nuwamba,1993

An fara bugawa a shekarar 1994
(Gidan Dabino Publishers, Kano, Nijeriya)

An sake tsarawa da bugawa a shekarar 2014

Century Research and Publishing Limited
Kano–Nigeria

ABUBUWAN DA KE CIKI

					Shafi
Addu'ar Buɗewa	**:**	**:**	**:**	**:**	ɓii
Godiya	**:**	**:**	**:**	**:**	iɗ
Sadaukarwa	**:**	**:**	**:**	**:**	ɗi
Mashigi	**:**	**:**	**:**	**:**	ɗiii
Gabatarwa	**:**	**:**	**:**	**:**	ɗɓii
Tsakure	**:**	**:**	**:**	**:**	ɗɗi
SASHEN AKIDA DA IMANI			**:**	**:**	**1**
Mene ne Addini?	:	:	:	:	1
Mene ne Imani?	:	:	:	:	2
Mene ne Ihsani (Kyauta yi)?	:	:	:		3
Allahu	:	:	:	:	5
Sassan Imani	:	:	:	:	6
Siffofin Allah Wajibai	:	:	:	:	7
Siffofin Allah Korarru	:	:	:	:	8
Siffar Allah Ja'iza	:	:	:	:	9
Taƙaita Aƙidojin Musulunci	:	:	:		10
SASHEN HUKUNCE-HUKUNCEN IBADA			**:**	**13**	
Matsayin Ibada		:	:	:	:
14					
Wasu Nau'o'in Ibada a Rayuwa			:	:	18
Alwala da Yadda ake yin ta		:	:	:	28
Salloli na Farilla	:	:	:	:	30
Salloli na Nafila	:	:	:	:	30

Lokutan Salla : : : : 32
Salla da Shirya Mata : : : : 33
Siffar Salla : : : : 34
Lafazin Kiran Salla : : : : 35
Lafazin Iƙama : : : : : 36
Sallamar Fitar Salla : : : : 40
Salloli na Farilla da Bishiyarsu : :
41
Sallolin Nafila : : : : 42
Farillan Salla : : : : 43
Sunnonin Salla : : :
44
Mustahabban Salla : : : 44
Abubuwan da ke Ɓata Salla : : : 45
Lalurar da ke sa a yi Ba'adi a Salla : : 45
Lalurar da ke sa Kabli : : : 45
Lalurorin da ba su da Kabli ko Ba'adi : 46
Jadawalin Yawan Raka'o'i a Sallolin
Farilla da Nafila : : : : 46
Azumi : : : : : 47
Ragwanta Shan Azumi : : :
48
Farillan Azumi : : :
48
Sunnonin Azumi : : : 48
Abubuwan da ake so ga mai Azumi : : 49
Hajji : : : 49
Rukunan Hajji : : : 49

Farillan Hajji : : : 49
Sunnonin Hajji : : : 50
Zakka : : : 50
Nau'o'in Zakka : : : 50
Farillan Zakka : : : 51
Ladubban Zakka : : : 51
Waɗanda ake ba Zakka : : 51

SASHEN WASU
AYYUKAN RAYUWA CIKIN IBADA : 52
Sakamakon Wasu Ayyukan Ɗan'adam : 52
Maganin Cutar Zunubai : : : 53
Wasiyyar Ubangiji ga Manzonsa, sallallahu alaihi wa sallama Don Sauran Mutane su Kwaikwaya : : : : 54
Riƙo da Halaye Guda Biyu : : : 54
Kwaɗaitarwa kan Aikata Alheri : 55
Baza Himma a Cikin Ibada : : 56
Musibu Uku na Karshen Duniya : : 56
Sakamakon Wulaƙanta Abubuwa Guda Biyar : 56
Mutanen Kwarai da Ashararai : : 57
Mace mai Haila : : : 58
Bin Umurnin Miji ga Mace : : : 58

Sakamakon Rashin bin Umurnin Miji ga Mace : 59
Sakamakon Matar da ke Kallafa wa Mijinta Abin da ba ya Iyawa : : : 59
Sakamakon Fitar Mata ba Tare da Sanin Miji ba ko Miji ya Bari ta Sanya Turare ta Fita : 59
Mata mai Kyautata wa Mijinta : : : 60
Wasu Mata da Sakamakon Ayyukansu : 60
Kafa Hujja da Mutane Huɗu : : : 62
Alamomin Tashin Kiyama : : : 63

SASHEN SIRAR ANNABAWA DA MANZANNI : 66
Halittar Mutane da Annabawa da Manzanni : 66
Sirar Annabi Muhammadu, Sallallahu Alaihi wa sallama : : : 71
Haihuwar Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa sallama : : : 72
Gari da Kabilar Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa sallama : : : 72
Nasabar Manzon Allah , Sallallahu Alaihi wa sallama, Mai Girma : : 73
Kuruciyarsa da Wasu Halayensa : : 73
Rainonsa da Tarbiyyarsa da Kiransa : : 75
Abubuwan da Manzon Allah, Sallallahu

Alaihi wa sallama, ya zo da su : : 76
'Ya'yan Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa sallama : : : 76
Matan Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa sallama : : : 77
Wasu Dangin Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa sallama : : : 78
Abubuwan da Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa sallama, ya Keɓantu da su : : 78
Wasu Ɗabi'un Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa sallama : : : 79
Wasu Daga Cikin Mu'ujizojin Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa sallama : : 80
Fasahar Harshen Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa sallama : : : 81
Wafatin Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa sallama : : : 84

SASHEN WAKOKIN KOYAR DA IBADA : 85
Waƙar Tallafi : : : 85
Waƙar Tariyar Baƙi Daga Ɗalibai : : 87
Waƙar Gane Ubangiji : : : 88
Waƙar Yarda da Musulunci : : : 89
Waƙar Matakan Addinin Musulunci : : 90
Waƙar Kabari : : : 91
Waƙar Tuni da Ranar Tashin Kiyama: : 96

SASHEN WAKOKIN YABO DA BEGEN

MANZON ALLAH : : : : 98

Waƙar son Manzon Allah, Sallallahu Alaihi Wasallama : : : 98

Waƙar ya Rabbi Salli ala al-Musɗafa : 99

Waƙar Manzon Allah Rasulullah : : 101

Waƙar Ɗahana Rasulullah : : : 106

Waƙar Al'arabiyul Hashimiyyu Muhammadi : 108

Waƙar Rasulu Abin Biya : : : 112

Waƙar Rasulu Manzon Tsira : : : 114

Waƙar Neman Ceton Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa Sallama : : : 116

Kammalawa : : : : 119

Manazarta : : : 124

Rataye: Jerin Wasu Tambayoyi : : 126

ADDU'AR BUƊEWA

Bismillahir Rahmanir Rahim

Yabo da godiya masu tarin yawa su tabbata ga Allah da ba za mu iya ƙididdige yawansu ba, tsira da amincin Allah su kasance ga Annabin shiriya, cikamakin Manzanni, wanda ya isar da amanar da aka ɗora masa, ta Manzanci, ya tsayar da hujja a kan mutane domin wanda zai ɓata ya halaka a kan dalili, shi kuma wanda zai rayu bisa gaskiya, ya rayu a kan bayyananne dalili, Allah shi ne mai ba da kyakkyawan ƙarshe. Allah ka yi tsira ga Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, da alayensa kamar yadda ka yi tsira ga Annabi Ibrahim, alaihis salam, da alayensa. Ya Allah ka yi albarka ga Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, da alayensa kamar yadda ka yi albarka ga Annabi Ibrahim da alayensa, lalle kai godadde ne kuma mai ɗaukaka.

Allah ka yi mana baiwa da hikimarka, ka yalwata mana rahamarka, ka lulluɓe mu da jinƙanka, ya mafificin mai rahama. Allah ka fitar da mu daga cikin duhun baƙin ciki, ka ba mu hasken fahimta, ka buɗa ƙirjinmu da sani da ma'arifa, ka kyautata halayenmu, ka ba mu ikon yin haƙuri, mu zama cikin bayinka masu kaifin nutsuwa. Allah ka buɗa mana ƙofofin arzikinka da karimcinka da baiwarka, ka inganta mana rayuwarmu daga taskokin rahamarka da jinƙanka, ya Ubangijin talikai.

Allah ka haskaka zukatanmu da albarka *Alƙur'ani* mai tsarki ka buɗa mana ƙirjinmu da albarkarsa, ka sauƙaƙa harshenmu wajen fahimtarsa, ka sanya jikinmu ya jiɓince shi, ya zama abokin hulɗarmu a ko da yaushe. Allah ka ƙarfafa zuƙatanmu da albarkar *Alƙur'ani*, ba mu da wata dabara ko

hikima, sai daga wajenka ya Allah, Allah ka dube mu da jinƙanka, ka ba mu cikawa da imani, ka yi mana kyakkyawan ƙarshe, amin.

Allah ka warkar da mu daga cututtuka na zuciya da na jiki da albarkar *Alƙur'ani*, ka ba mu ikon neman ilmin sanin hanyoyin yi maka bauta, ka yi mana ni'ima don albarkar sirrin da ke cikin *Alƙur'ani*. Allah ka ba mu cikawa da imani, mu tashi muna tare da shi. Allah ka kiyaye mu daga azabar wuta, ka tsare wuyayenmu daga aikata ayyukan assha. Allah ka shiryar da mu, ka kuma shiryar da 'ya'yanmu da 'ya'yan 'ya'yanmu da dukkanin zuriyar Musulmi baki ɗaya, amin.

Allah ka yi mana gafara ga iyayenmu da dukkan Musulmi maza da mata, waɗanda suke a raye da waɗanda suka rigaye mu gidan gaskiya. Ya Allah kada ka bar mu da zaɓin kanmu, Allah ka yi mana jagora ga dukkan ayyukanmu, kuma ka kyautata al'amuranmu. Allah ka ɗaukaka Musulunci ka ƙasƙantar da kafirci. Allah kada ka ba duk mai yi wa addinin Musulunci zagon ƙasa wani ƙarfi da tasiri, Allah ka rusa al'amarinsa. Allah ka ba Musulmi da Musulunci galaba a duk inda yake a bayan ƙasa, amin.

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin halittu, mai rahama mai jinƙai, mai mulkin Ranar Sakamako. Allah kai kaɗai muke bautawa, kuma kai ne kawai muke neman taimakonka. Ka shiryar da mu ga hanya madaidaiciya, hanyar waɗanda ka yi wa ni'ima, ba waɗanda aka yi wa hushi ba, kuma ba ɓatattu ba, amin.

Allah ka yi mana jagora a wannan aiki da dukkan ayyukanmu na yau da gobe na duniyarmu da lahirarmu. Allah ka sa mu dace ka kuma yi mana taimako, amin.

GODIYA

Bayan godiya ga Allah, mai girma da ɗaukaka, da salati ga Annabin Rahama, Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, ina yin godiya ga duk wanda ya sa hannu har Allah ya ƙaddari wannan littafi ya zamanto kamar haka.

Haka kuma ina gode wa duk wani wanda ya ba da shawarwari ko wata taimakawa ta musamman don ƙara inganta wannan aiki kamar Alhaji Muhammadu Tukur Tsoho da Malam Bello Muhammad Ɗankullum da Malam Aminu Salmanu da Malam Garba Sa'idu Akwa da Malam Habib Alhassan da Hajiya Hauwa Kulu Habib Alhassan da Alhaji Jazuli Musa da Malam Usman Ladan Kurya da Alhaji Ibrahim S. Alhassan da Alhaji Salisu Ahmad Funtua da Alhaji Rabi'u Ahmad Funtua da Farfesa Ibrahim M. Abdullahi Malumfashi da Malam Bashir Sanda Gusau.

Ina kuma gode wa Farfesa Muhammadu Sani Zahraddeen da Farfesa M.K.M. Galadanchi da Farfesa Ibrahim Yaro Yahaya da Malam Muhammad Al'amin Umar da Farfesa Isma'il Abubakar Tsiga da Farfesa Sa'idu Ahmad Ɓaɓura da Alhaji Muhammadu Sani Ibrahim da Farfesa Abba Rufa'i da Farfesa Bello Sa'id da Farfesa Muhammad Auwal Abubakar da Farfesa Ɗahiru Yahya da Farfesa M. D. Sulaiman. Allah ya saka musu da alherinsa, amin.

Matuƙa nake gode wa ɗaliban *Al-Madrasatul Lubabiyya Lihidayatil Adfal,* da malamarsu Malama Lubabatu Sa'idu Muhammad da Malam Muhammad Nuraddeen Umar Gusau da Malam Nasiru Muhammad Gusau, saboda shirye-shiryen da nake yi musu na lokacin Maulid na shekara-

shekara ne ya haifar da wannan littafi. Ba zan taɓa mantawa da ayyukan koyarwa a wannan makaranta ba.

Tare da nema masa gafara, nake yin godiya zuwa ga marigayi Alhaji Muhammadu Lawal Mande, Mutawallen Gusau, Allah ya kyautata makwancinsa, ya yi rahama a gare shi, amin.

Malam Abdu Ado Sharaɗa wanda ya buga aikin da na'urar kwamfuta, Allah ya biya shi ladan gudunmuwarsa. Sai kuma Yusha'u Sa'idu Muhammad wanda ya gyaggyara aikin a kwamfuta da kuma sauran waɗanda suka taimaka wajen ɗab'in littafin, kamar yadda yake a haka, musamman Malam Ado Ahmad Gidan Dabino, mai Gidan Dabino Publishers, Kano da Malam El-Hussein Shu'aibu Burji, mai Kamfanin Century Research and Publishing Limited, Kano. Muna roƙon Allah ya saka musu da alheri, kuma ya sanya al'amuransu su dinga tafiya cikin sauƙi, amin.

Allah ya ƙara ba mu juriya da ƙarfin guiwar ci gaba da aiwatar da irin waɗannan ayyuka ga addininmu, amin. Na gode.

Sa'idu Muhammad Gusau
Dip(ABU), B.A.; M.A.; Ph.D. (BUK; 1989) Farfesa(BUK;2000)
Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya,
Jami'ar Bayero, Kano
Asabar, 28 ga Watan Yuni, 2014 M.
Daidai da 1 ga Watan Ramalan, 1435 H.

SADAUKARWA

Da yardar Allah, mai girma mai ɗaukaka, nake sadaukar da wannan littafi ga ɗaliban Al-Madrasatul Lubabiyya Lihidayatil Aɗfal da malamarsu, Malama Lubabatu Alhaji Buba Maigoro Gusau.

Haka kuma ina sadaukar da aikin zuwa ga iyayenmu maza waɗanda suka yi mana tarbiyya ta gari, Malam Muhammadu Ɗankullum da Alhaji Abubakar (Buba) Maigoro da iyayenmu mata dukkansu da malamanmu dukkansu.

Ina roƙon Allah ya gafarta wa iyayenmu, ya ƙara musu ni'ima, ya sanya Aljannal-Firdausi makomarsu madauwamiya, amin.

MASHIGI

Ya Rabbi Sarki Kahharu,
Allahu ne tun azliyya.

Ga sallama da salati nan,
Gun Musɗafa Manzon shirya.

Alai, sahabbai, 'ya'yansa,
An gai da su duk kulliya.

Bayan sana'i da salati,
Sai albishir kan tarbiyya.

Shi wanga talifi namu,
An yo shi ba wata fariyya.

Domin ya zam na tunatarwa,
Bisa kan haƙi na ibadiyya.

Ba yau ba ko da tun can da,
Da akwai shari'a abdiyya.

Saukarta duk da ibadarta,
Allah gwani shi ya shirya.

Jama'a mu daure gun koyon,

Ilmin ibada mui gaya.

Da maza da mata danginmu,
Dukkanmu yara har manya.

A biɗe shi ilmi farlun ne,
Na sanin ibada je koya.

Manzo, Rasulu ya furta,
Nemar shi ilmi sa niyya.

Ɗalabul ilmu haƙƙun ne,
Ko da a Chana da Indiyya.

Wannan faɗa fa ta Manzo ce,
Ga maza da mata kulliya.

Mu riƙe da kyawo mui koyi,
Bisa wanga addinin shirya.

Wallai mu san ita ko shari'a,
Mahadî gare ta ibadiyya.

Harkar ibada sai hukmi,
Su za a gwama ba gayya.

Mun san ibada aiki ne,
Da ake sanin sa da an koya.

Manzonmu kana shi ya ce,
Addin mu daure kwaikwayya.

Ke nan ashe in mun gane,
Bauta mu san sai ilmiyya.

In kai ibada ba ilmi,
Banza kake yi sai jinya.

Ba za a sam wata lada ba,
Sai dai zunubi don ƙuiya.

Kai dai Musulmi an yo ka,
Don kai riƙo da aƙidiyya.

Daure ka nemi sanin shari'a,
Kame halal ƙi haramiyya.

Kalma ta tauhid ne farko,
Sannan da salla duk sanya.

Kono da zakka sai saumu,
Haji ka je shi fa sau ɗayya.

Rukunai na imani na nan,
Da zama na hulɗar nan duniya.

Ilmi da neman koyonsa,
Zai sa a ƙaru da tarbiyya.

Shi duk abin da mutum ya iya,
Ni'ima gare shi a tun duniya.

Dukkan Musulmi nai jam'i
Ku riƙe ta hanyar ilmiyya.

Allah ya saka yai budî,
Ga waɗanda sun kai tamayya.

Yara da manya mun gode,
Fata muke da ku sam shirya.

Bayanmu ko ka daɗo haske,
Ilmi da kyawon zuriyya.

Mai wagga waƙa shi dai ne,
Gusau Sa'idu yas shirya.

Zan dakata in sa aya,
Allah ka sa mu a kan shirya.

Baitinta sittu salasuna,
An yo su ba wata jayayya.

GABATARWA

Da sunan Allah, Mai Rahama, Mai Jinƙai

Ka ce (Allah ya ce), ya bayina waɗanda suka yi imani, ku bi Ubangijinku da taƙawa. Waɗanda suka kyautata a cikin wannan duniya suna da sakamako mai kyau, kuma ƙasar Allah mai faɗi ce. Masu haƙuri kawai ake cika wa ijararsu, ba da wani lissafi ba (Zumar, aya ta 10).

Ka yi karatu da sunan Ubangijinka, wanda ya yi halitta. Ya sanar da mutum abin da bai sani ba (Alaƙ, aya ya ta 1 da ta 5).

Ilmin shari'a ya kewaye dukkan ilmi a bayan ƙasa, da shi ne zukata ke buɗuwa da rayuwar duniya da lahira. Sannan kuma sai an san shi, sannan za a fahimci kyakkyawar hanyar yi wa Allah bauta tare da bin ƙa'idojin da suke zagaye da yin haka. Allah ya umurci bayinsa da su nemi ilmin yi masa bauta wadda domin ta kawai aka halicce su. Allah yana cewa, '*Ban halicci aljan da mutum ba, sai don su bauta mini'.* Ita wannan bauta wadda ta ƙunshi dangogin shari'a daban-daban ba a yin ta sai an koye ta. Shi wannan ilmi kuma Allah ne yake sanar da bayinsa shi, ya hore musu fahimtarsa. Dubi yadda Allah ya sanar da Annabi Adamu, alaihis salam, dangogin ilmin da bai sanar da mala'iku ba. Su da kansu mala'iku suke cewa:

Suka ce (Mala'iku): 'Tsarki ya tabbata a gare ka ! Babu sani a gare mu face abin da ka sanar da

mu. Lalle ne kai, kai ne masani, mai hikima (Baƙara, aya ta 32).

Domin haka, Allah shi ne mai cusa ilmi a cikin zukatan bayinsa, amma sai ya ba su iko da damar tashi tsaye su koye shi. Shi ya sa duk wanda ya nace wa neman ilmi, Allah kuwa zai sanar da shi. Ta haka ne ma Allah ya nuna ba ya son raggo wanda ba ya aiki da damar da aka ba shi. Kuma ya ƙyamaci wanda zai yi ƙoƙarin yi masa bauta a jahilci bisa son zuciyarsa ba tare da ya koya ba. Allah yana son masu kyautata ayyukansu saboda sun san za su haɗu da shi watan watarana. Shi ne yake cewe:

Waɗanda suka tabbata cewa lalle ne su masu haɗuwa ne da Ubangijinsu, kuma lalle ne su zuwa gare shi masu komawa ne (Baƙara, aya ta 46).

Daga nan kuma ya yi tsoratarwa ka da a ɓoye gaskiya a fifita ƙarya, ka da mutum ya zauna cikin ƙarfafa ayyukan assha a kan na sambarka. Allah ya ce:

Kuma kada ku lulluɓe gaskiya da ƙarya, kuma ku ɓoye gaskiya, alhali kuwa kuna sani (Baƙara, aya ta 42).

Wasu abubuwan da Allah, tabaraka wa ta'ala, yake so su ne:

Kuma ku tsayar da salla, kuma ku bayar da zakka, kuma ku yi ruku'i tare da masu yin ruku'i (Baƙara, aya ta 43).

Kuma ku nemi taimako da yin haƙuri da salla, kuma lalle ne ita (salla), haƙiƙa, mai girma ce, face fa a kan masu tsoron Allah (Baƙara, aya ya 45).

Allah ya ba da dama ga wasu mutane da su tashi tsaye ga yin koyarwa da wa'azi da faɗakarwa da sanar da Musulmi matakan yi wa Allah bauta da gaya musu hukunce-hukuncen Allah da kuma iyakokinsa da haddodinsa. Su ma waɗannan masu wannan koyarwa ba a bar su a haka ba, Allah ya yi musu faɗakarwa su ma kansu da su dinga yin ayyukan alheri da ibada kamar yadda suke horon jama'a da yin haka. Shi ne Allah yake gaya musu:

Shin kuna umurnin mutane da alheri, kuma ku manta da kanku, alhali kuwa kuna karatun littafi? Shin ba za ku hankalta ba? (Baƙara, aya ta 44).

Ibada wajiba ce ga dukkan Musulmi, namiji da mace, baligi da baliga da sharuɗɗan addini suka ɗoru a kansu. Shi ma neman ilmi na ibada farilla ne kamar yadda Annabin Rahama, sallallahu alaihi wa sallama, yake cewa:

Neman ilmi farilla ne a bisa dukkan Musulmi (Namiji da Mace). Sannan kuma da inda Manzo yake faɗi: *ku nemi ilmi ko da ta kai sai an tafi birnin Sin*

An yi tunanin gabatar da wannan littafi kamar yadda aka fara nunawa a godiya a sakamakon shirin Maulid da na yi shekaru goma aƙalla ina tsara wa *Al-Madrasatul Lubabiyya*

Lihidayatil Aɗfali. Na ga ya dace karance-karance da ɗaliban suka yi in haɗe su a waje ɗaya don gudun kada su watse, kuma a sami abin karantawa nan gaba. Daga nan ne na yi wannan azama na daɗa inganta waɗannan abubuwa na ƙara na ƙarawa na rage wasu, sai suka zama wannan littafi.

An raɗa wa aikin suna *Mu Koyi Ibada,* musamman ganin abubuwan da suke tattare a cikinsa suna koyar da nau'o'in ibada ne da hukunce-hukuncenta. Wannan shi ne littafi na ɗaya, da yardar Allah, sauran na biyu da na uku za su biyo baya.

An rarraba littafin zuwa manyan sassa da suka haɗa da sashen aƙida da imani da sashen hukunce-hukuncen ibada da sashen wasu ayyukan rayuwa a cikin ibada da sashen sirar Annabawa da manzannin Allah da sashen waƙoƙin koyar da addinin Musulunci da sashen waƙoƙi na yabo da begen Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama.

Ina roƙon Allah, mai rahama mai jinƙai, ya sa wannan aiki ya zama mai amfani ga dukkan al'ummar Musulmi, musamman yara, ɗaliban makarantun Islamiyoyi da na firamare da na sakandare da sauran duk mai sha'awa da kishin addinin Musulunci.

TSAKURE

Shari'a hanya ce bayyananniya wadda Allah ya shimfiɗa kuma ta ƙunshi hukunce-hukunce da dokoki da suka danganci rukunan imani da bauta da kyautatawa da ma'amala da tsarin rayuwa da makamantansu zuwa ga bayinsa don tabbatar da jin daɗin rayuwasu duniya da lahira. Ibada kuma ta shafi aiki da gaɓoɓin jiki wajen yi wa Allah bauta da kyauta yi a cikin dukkan dangogin rayuwar ɗan'adam ta bin shari'a.

Abubuwan da ke tattare cikin wannan littafi suna koyar da wasu sassan ibada a cikin shari'ar Allah da suka haɗa da sashen aƙida da imani da sashen hukunce-hukuncen ibada, kamar tsarki da alwala da salla da azumi da hajji da zakka, da wasu ayyukan rayuwa cikin ibada da sirar Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, da wasu waƙoƙin yabo da begen Manzon Allah da wasu waƙoƙin koyar da ibada. An tsara wannan littafi ne domin yara, musamman 'yan makarantar Islamiyoyi da na firamare da na sakandare da sauran ɗalibai da masu son su koyi wani abu daga cikin sha'anin addinin Musulunci.

1

SASHEN AKIDA DA IMANI

Babban abin da mutum zai koya ya sami ni'imarsa ta har abadiyya tun daga duniyarsa har zuwa lahirarsa, shi ne, sanin Allah Jalla-Jalalahu. Akan gane Ubangiji, Allahu, daga halittunsa da ya yi, tun daga ta kan yadda aka tsara halittar mutum kansa da dabbobin da yake gani, yake tare da su, ko ya ji labarinsu da itatuwa da tsirrai da sauransu, ga su nan duk suna rayuwa lalle akwai wanda ya yi su. Shi ne kuma *Allahu*. Haƙiƙa wanda bai san Allah ba, ba wani abu da zai amfane shi daga cikin ayyukansa, sai nadama da taɓewa. Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, yana cewa "wanda ya yi wa Allah bauta, kafin ya nemi ilmin saninsa, ko da jijiyoyin jikinsa za su tsunke saboda tsananin ibada, ba abin da zai samu, sai nisanta daga mahaliccinsa, Allah".

Wannan shi ne sashe na farko wanda ya ƙunshi sha'anin imani da aƙida da kaɗaita Allah, subhanahu wa ta'ala. Imani da Allah da dukkan rukunansa shi ne zai ba mutum cikakken ruhin rayuwa da samun ni'imominta, da godabe shararre, miƙaƙƙe da zai kai mutum ga sa'ada. Daga cikin abubuwan da sashen ya ƙunsa akwai ma'anar addini da imani da ihsani. Akwai wani ɓangare da aka taƙaita aƙidojin tauhidi inda aka ci gaba da bayani a kan sassan imani da matsayin *Alƙur'ani* a Musulunci da ayyana siffofin Allah wajibai da mustahabai da ja'izai da sauran abubuwan da suka shafi tauhidi da aƙida.

Mene ne Addini?

Abubuwa guda uku ne suka haɗu suka yi addinin Musulunci, su ne kamar haka:

- Musulunci
- Imani
- Ihsani

Mene ne Imani?

Imani wani abu ne da yake ɗarsuwa a zuciya, sannan aiki ya tabbatar da shi. Domin haka, imani a Musulunci shi ne yarda da Allah, mahaliccin kowa da komi, wanda ke sanya hukunci bisa ƙudurarsa da ƙaddararsa. Sannan da yarda da Mala'ikun Allah da Littattafansa da Manzaninsa da Ranar Ƙarshe da Ƙaddara ta alheri ko ta sharri. Idan mutum ya sakankance da waɗannan rukunai na imani ya zama ke nan wanda ya miƙa wuya zuwa ga Allah da Manzonsa kuma su ne Annabin Rahama, Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, ya zo da su daga wurin Allah. Ashe Musulmi shi ne wanda ya yarda, ya sakankance da waɗannan abubuwan da Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, ya kawo wa duniya. Allah, tabaraka wa ta'ala, ya ce, Musulmi mumini shi ne:

"Wanda ya yi imani da Allah da Ranar Ƙarshe da Mala'iku da Annabawa".

Shi kuma wanda ba shi da imani shi ne wanda ya kafirce wa waɗannan abubuwa. Ya finjire musu, ya ƙi nuna yardarsa da amincewarsa. Allah yana cewa kansa:

"*Wanda ya kafirta (ya ƙi yarda) da Allah da Mala'ikunsa da Littattafansa da Manzanninsa da Ranar Karshe, haƙiƙa ya ɓata, ɓata kuma mai nisa".*

Wato ya yi nisa da rahamar Allah da jinƙansa. Allah ya kiyaye mu, Amin.

Imani yana da rukunoni har guda goma sha ɗaya, su ne kuwa:

- Imani da Allah
- Imani da Manzannin Allah
- Imani da Littattafan Allah
- Imani da Mala'ikun Allah
- Imani da Kaddara
- Imani da Aljanna
- Imani da Taukin Kausara
- Imani da Ranar Karshe[1]
- Imani da Siratsi
- Imani da Mutuwa da Hisabi
- Imani da Wuta[2]

Mene ne Ihsani (Kyauta yi)?

Ihsani ko kyauta yi shi ne ka bauta wa Allah kamar kana ganin sa, ko da yake ba ka ganin sa, ka san yana ganin ka. Daga Hadisin Umar ɗan Khaɗɗabi aka gano cewa, abubuwa guda uku ne suka haɗu suka gina addinin Musulunci, babu shakka, idan ɗayansu ya sumɓule babu addinin Musulunci. Akwai Musulunci ga aikata ayyukan ibada da gaɓoɓin jiki, kamar tsayar da salla da yin azumi da faɗar kalmar shahada

[1] Wato Ranar Tashin Kiyama.

[2] Allah ya kiyaye mu daga shiga wuta, amin.

da fatar baki da zuwa aikin hajji da karatun *Alƙur'ani* da ambaton Allah da sauransu. Sai kuma a gaskata duk abubuwan addini sun fito ne daga wajen Allah, sannan suka bayyana ta harshen Manzanninsa. Domin haka, Allah yake gaya wa Annabin Karshe, sallallahu alaihi wa salam:

> *"Abin saukarwa (Alƙur'ani) ne daga Ubangijin halitta duka. Kuma da (Muhammadu) ya faɗi wata magana, ya jingina ta gare mu. Da mun kama shi da dama. Sannan, lalle ne da mun katse masa laka" (Suratul Haƙƙa, aya ta 43 – 46).*

Allah kuma ya ƙara cewa:

> *"Ma'abucinku (Muhmamadu) bai ɓata ba, kuma bai ƙetare haddi ba. Kuma ba ya yin magana daga son zuciyarsa. (Maganarsa) ba ta zamo ba, face wahayi ne da ake aikowa. (Mala'ika) mai tsananin ƙarfi ya sanar da shi. Ma'abucin ƙarfi da kwarjini, sa'annan ya daidaita. Alhali kuwa yana a sararin sama mafi ɗaukaka" (Suratul Najmu, aya ta 2 – 7).*

Wannan ne ma ya sanya lokacin da Mala'ika Jibrilu yake sauko wa Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, da wahayi na *Alƙur'ani*, sai Allah mai sauƙaƙa abubuwa ya ce masa, ya daina nauyayar da kansa, da sannu za a jefa masa ambato ya gane shi sosai don ya isar da shi ga al'ummar duniya baki ɗaya. Dubi abin da Allah ya ce:

> *"Kada ka motsar da harshenka game da shi domin ka yi gaugawar riƙe shi (Alƙur'ani). Lalle*

ne wajibi ne a gare mu, mu tara shi, mu (tsare maka) karatunsa. To, idan muka karanta shi, sai ka bi karatunsa. Sa'an nan, lalle ne, wajibi ne a gare mu bayaninsa" (Suratul Kiyama, aya ta 16 – 19).

Ashe idan mutum ya kasance mai bin umurnin Allah ne, Allah zai dinga sauƙaƙe masa al'amuransa, ya zamanto kuma mai saurin ganewa da lura da nutsuwa, har ya iya ba wasu 'yan'uwansa Musulmi shawarwari kyawawa bisa shiriyar da ya samu daga Allah, maɗaukaki.

Daga nan kuma abu na uku a game da abubuwan da suka ɗinke waje ɗaya suka zama addinin Musulunci, shi ne yin ayyukan addini saboda Allah. Mai ibada ya kyauta yin ta, kamar yana ganin Allah tsaye a gaba gare shi, Allah yana cewa:

"Kuma ku bauta wa Allah, kuma kada ku haɗa wani da shi" (Suratun Nisa'i, aya ta 36). Kuma Ubangijinka ya hukunta kada ku bauta wa kowa face shi" (Suratul Isra'i, aya ta 23). "Kada ka sanya wani abin bautawa na daban tare da Allah, har ka zauna kana abin zargi, yarɓaɓɓe" (Isra'i, aya ta 22).

Bayan kyauta yin bautar Allah ta bin umurce-umurcensa da kamewa daga hane-hanensa, akwai kuma wasu nau'o'in mutane da aka ce Musulmi ya kyautata musu ya yi musu ihsani kamar mahaifa, iyaye maza da mata, da maƙwata

da matalauta da miskinai da matafiya da ma'abota kusanta[3] da abokai da sauransu. Dukkan waɗannan dangogin mutane da nau'o'in ihsanin da za a iya yi musu gwargwadon darajarsu da kuma halin da mutum yake da shi.

Allahu

Allahu shi ɗaya yake, Ubangiji[4], kuma mai yin halitta, wato mahalicci. Allahu yana da siffa ta ɗaiɗayantaka, guda-guda ne da bai yi kama da kowane irin mahaluki ba. Allahu shi ne ake nufa da ibada (bauta) da gaskiya, ba shi buƙata ga kowane irin waninsa, kuma kowa yana da buƙata zuwa gare shi. Ba a haife shi ba, bai haifa ba. Samuwarsa wajiba ce, ana kuma gane shi ta yin la'akari da halittunsa. Allahu shi ne wanda yake sanya rayuwar duniya da ta lahira da abin da ke tsakaninsu da sama da ƙasa su dinga tararrufi. Allah ya siffanta kansa a cikin Suratul – Ikhlasi da cewa:

> *"Ka ce "Shi ne Allah maɗaukaki, Allah wanda ake nufinsa da buƙata, bai haifa ba, kuma ba a haife shi ba, kuma babu ɗaya da ya kasance tamka a gare shi" (Suratul-Ikhlas).*

Allah shi ne mai rahama mai jinƙai, kuma shi gafurun ne. Wanda ya bi umurninsa ya dace, wanda kuma ya bijire wa umarninsa ya taɓe[5].

Sassan Imani

---

[3] Wato kamar 'yan'uwa, maza da mata, na kusa da na nesa da masu yi wa mutum hidima da sauran mutanen da ake tare da su a zama da ma'amalar rayuwa.

[4] Wato mai haƙƙin sarrafa kowace irin halitta.

[5] Allahu shi ne mai ba da zaɓin *yi* ko *bari*, mai Aljannah mai Wuta, mai yin aiki bisa nufinsa da iradarsa, mai ƙaddara komai bisa ikonsa, mai Al'arshi da Kursiyyu.

‘Yan’adam dukkansu fararru ne, wanda ya halicce su, shi ne Allah, mai girma da ɗaukaka, samuwa wajiba ce a gare shi, daɗaɗɗe ne wanda ba shi da farko, wanzajje kuma dauwamamme da rashi bai gabace shi ba, kuma wanda ba shi da ƙarshe wato ba a iya ayyana farko nasa ko ƙarshe nasa ba. Ya saɓa kamannin kowane nau’i na halitta, tsayayye ne da tsayuwarsa, shi kaɗai yake, iko da nufi da ilmi da rayuwa da ji da gani da magana duk a gare shi suke. Ba shi da bagire ko wani sashe da yake zaune.

Wajibi ne Musulmi ya tabata Allah samamme ne tun azaliyya. Kamar yadda ya riga ya gabata, Allah shi kaɗai yake a zatinsa da siffofinsa da ayyukansa. Mai iko ne da iko, mai nufi da nufa. Mai sani da sani, rayayye da rayuwa, mai ji da ji, mai gani da gani, mai magana da magana, mai zaɓi da aikata aiki ko barinsa. Kamala da cika wajibi ne a gare shi, tawaya kuma korarriya ce a gare shi da zatinsa.

Haka nan Manzanninsa dukkansu tun daga Adamu, alaihis salam, har zuwa ga Manzon Allah, Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, masu gaskiya ne da a kullum za a dinga gaskatawa. Su masu amana ne, sun kuma isar da manzancin da aka aiko su da shi zuwa ga sauran ‘yan’adam. Cika irin ta mutuntaka wajiba ce a gare su, tawaya irin ta ɗan’adam korarriya ce a gare su. Halal ne kuma ja’izi a gare su, su ci, sannan su sha, su yi aure, su yi hulɗar ciniki ta saye da sayarwa. Kuma suna iya kamuwa da rashin lafiya wadda ba za ta juyar da hankalinsu ko ta kai su ga wata tawaya ko naƙasa ba.

Allah ya sanya ajali da mutuwa a tsakanin halittunsa, sannan ya ƙaddara tashi bayan mutuwa inda za a yi wa kowane mutum hisabi. Ya kuma sanya zaman kabari[6] kafin a

[6] Wato zaman kewa kafin a tashi zuwa *tsayuwa.*

yi busar tashin ƙiyama wadda za a umurci Mala'ika Israfilu ya yi ta. A cikin kabari akwai tambayoyi da Munkari da Nakiri za su yi wa mamaci inda za su tamayi Ubangijinsa da addininsa da Manzonsa da ibadarsa da sauransu. Idan mutum mumini ne ya sami ni'imar kabari, idan kuwa fajiri ne ya sami azabar kabari. Allah kuma ya halicci Aljanna ga mai rabo, wanda ya yi ayyuka na alheri da wuta ga wanda ya taɓe, wanda bai bi umurnin Allah ba.

Wajibi ne ga kowane mukallafi wato baligi, ya yi imani da waɗannan abubuwa, kuma neman ilmin aiki da su wajibi ne ga kowane ɗaiɗaikun mutane.

Siffofin Allah Wajibai

Allahu, subhanahu wa ta'ala, ya keɓantu da wasu siffofi waɗanda ba yadda za a yi su kankaru a gare shi. Waɗannan siffofi da suka wajaba ga Allah guda ashirin ne. Ga su kamar haka:

Samuwa
Dauwama[7]
Wanzuwa
Sassaɓa wa ga Halittunsa
Dogaro da Zatinsa
Kaɗaita
Iko
Nufi
Sani
Rayuwa
Ji
Gani

[7] Wato *gabata*, Allah ya gabata tun azaliyya.

Zance[8]

Kasancewar Allah:
Mai Iko
Mai Nufi
Mai Sani
Mai Rayuwa
Mai Ji
Mai Gani
Mai Magana[9]

Siffofin Allah Korarru[10]

Akwai kuma wasu siffofi guda ashirin da ba za a iya danganta su izuwa ga Allah ba. Waɗannan siffofi sun koru ga Allah, su ne kuma:

Rashi
Faruwa
Karewa
Kamancewa
Bukata
Tarayya
Gajiyawa
Tilastawa[11]
Jahilci

---

[8] Wato *magana*, Allah yana magana irin tasa.
[9] Allahu yana da waɗannan siffofi kuma suna gudana ne saɓanin yadda suke gudana a wajen halittun da ya yi kamar ɗan'adam da dabbobi da sauransu. Kuma babu bukatar bin ƙwaƙƙwafi domin a gano yadda suke a wurinsa, sai dai a bi ta kan halittunsa idan ana so a daɗa gane shi.
[10] Wato mustahilai waɗanda ba za a taɓa danganta su ga Allah ba.
[11] Wato ikrahi kamar a turke mutum kan sai ya yi wani abu. Wannan siffa ta tilastawa ta koru a wajen Allah.

Mutuwa
Kurmantaka
Makanta
Bebantaka

Zamantowar Allah:

Gajiyayye
Mai Ki
Jahili
Matacce
Kurma
Makaho
Bebe[12]

Siffar Allah Ja'iza

Allah, mai rahama mai jinƙai, yana da siffa guda ɗaya wadda ta zama ja'iza a gare shi. Ja'izi ne ga Allah ya aikata duk abin da ya yi nufi ko ya buƙace shi, ko kuma ya ƙi yi. Yi da bari zaɓi ne na Allah daga zatiyyarsa, babu wani mai tilasta masa ga yin wani abu ko barinsa. Shi mai aikata abin da yake so ne ko barinsa, bisa ikonsa da kuma ƙudurarsa da iradarsa.

Haƙiƙa, babu kokonto a kan samuwar Allah, kuma babu musantawa shi ne mahaliccin kowa da komi a sararin samaniyya da ƙarƙashin ƙasa da abin da ke a tsakaninsu, da gabas da yamma da kudu da arewa da sama da ƙasa. Allah ba shi da farko, ba shi kuma da ƙarshe, babu wani abu da ya yi kama da shi, shi mai ji ne kuma mai gani. Su kuwa dukkan mutane masu buƙatuwa ne zuwa gare shi, amma shi Allah wadatacce ne mayalwaci, godadde.

[12] Allahu ba shi da ko ɗaya daga cikin waɗannan siffofi.

Allah abu ɗaya ne, kuma wahidun, mu sani da akwai alloli da yawa a cikin duniya, da yanzu ta gama lalacewa. Shi kuma Allah mai iko ne a kan dukkan komi, mai yin aiki bisa nufinsa da muradinsa, ga shi mai cikakken ilmi bisa dukkan komi, masanin abin da ya faku kuma mai shaidarwa. Shi Allah rayayye ne, ba ya mutuwa, ba ya barci ko gyangyaɗi ko mantuwa. Allah yana tare da kowace irin halitta, yana jin ta kuma yana lura da abin da take yi.

Allah gwani ne buwayi gasa, gagara misali, mai yin magana da wanda ya so, ko aikata zaɓinsa. Ubangiji Allah yana halittar abin da yake so, sannan ya zaɓa. Domin haka, da Allah babu shi wato korarre ne, da ba a sami kowa da komi daga cikin abubuwan halittawa ba. Idanu sun tabbatar da samuwa da wanzuwar Allah[13].

Taƙaita Aƙidojin Musulunci[14]

Kamar yadda aka bayyana a baya, Allah shi ne buwayi gasa gagara misali, kaɗaitacce wanda ba shi da abokin tarayya, ba a haife shi ba, bai haifa ba. yana da siffofi da halaye da sunaye irin nasa da ba su da gamaɗɗa da kowace irin halitta. Shi ne mai zaɓi a cikin ayyukansa. Allah ne mahaliccin kowa da komi ta kalmomin *kun fa yakun[15]*. Allah ya halicci mutane da aljannu, ya ɗora musu yi masa bauta. Allah mai

[13] Halittu da yadda suke motsi, suna sassauyawa sun nuna akwai wanda yake tafiyar da su, shi ne *Allahu* wanda yake sanya abu maras motsi *sandararre* ya yi motsi, ya kuma dinga jujjuyawa.

[14] A wannan ɓangare ne aka yi bayanin ***Musulunci*** da aƙida ta Musulunci.

[15] Wato zamo sai ya kasance.

girma da ɗauka yana cewa; “Ban halicci aljani da mutum ba sai don su yi mini bauta” (Sura ta 51, aya ta 56-58).

Allah, madauwami, wanzajje, ya gindaya bautarsa bisa hanyar addinin Musulunci. Ya shar’anta wa mutane Musulunci ya zama tafarkin bauta, inda aka ayyana daki – daki matakan yin wannan ibada[16]. Allah ya wajabta wasu haƙƙoƙi na tantance matsayin kowa da rarrabewa tsakanin Allah mahalicci da bayinsa abin halitta, da kuma a tsakanin ‘yan’adam, a ya-su-ya-su. Sannan Allahu, cikin ikonsa da rahamarsa, ya zaɓi wasu ayyanannun mutane ya ɗora musu nauyin jagorancin isar da wannan aiki, su ne ake kira Manzanni. Manzanni su ne Allah ke yi musu wahayi da abin da yake buƙatar bayinsa su yi, su kuma sai su isar da shi a gare su[17]. Ta haka suka zama Manzanni ko Jakadun Allah, maɗaukaki.

Har wa yau, kamar yadda ya gabata, Musulunci shi ne miƙa wuya a aikace kuma a bayyane bisa kwatanta bin umurce-umurce da hane-hanen da Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya zo da su ga duniya baki ɗaya. Mutamen da ya miƙa wuyansa ga wannan al’amari na Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, shi ne ake kira Musulmi.

Su kuwa Manzanni, zaɓaɓɓu ne na bayin Allah daga cikin mutane, ya aiko su ga sauran halitta don su shiryar da su zuwa ga abin da yake alheri a rayuwarsu ta duniya da ta lahira. Annabi, shi ne mutum namiji, ɗa, mai hankali mai lafiya da aka yo wa wahayi na shari’a, amma ba a ce ya kira mutane zuwa gare shi ba kamar Idris da Yunus da Dawud da Yahya da Shu’aibu da sauransu. Manzo kuwa shi ne Annabin

---

[16] Ibada ta ƙunshi abubuwa biyu manya akwai *usulu* wato asali da *furu’u* wato rassa.

[17] Wato *bayi,* ‘yan’adam.

da aka yi wa wahayi na shari'a kuma aka umurce shi da ya watsa shi a tsakanin mutane, kamar Annabi Ibrahim da Nuhu da Isa da Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, da sauransu. Manzanni suna da siffofi wajibai da suka haɗa da gaskiya da amana da isar da manzanci da kaifin hankali, sannan da kishiyoyinsu korarru wato ƙarya da hiyana (rashin amana) da ƙin isar da manzanci da dabbalci[18].

Sannan kuma dole ne Musulmi ya amince da wanzuwar Mala'iku, kuma su ma bayi ne da ake girmamawa. Allah ya sanya jukunkunansu mabambanta, kamammu daga buƙatar abinci ko abin sha ko jin sha'awa ko haifefeniya. Ba a yi su ta yadda za a tantance maza ko mata a tsakaninsu ba. ba su yi wa Allah tawaye a kan abin da ya hore su da shi, kuma su masu aikata abin da ya umurce su da shi ne nan take. Sannan suna iya yin tafiya mai nisa a cikin ɗan lokaci ƙanƙane. Allah, subhanahu wa ta'ala, ya ce "An sanya Mala'iku, Manzanni, ma'abota fika-fikai guda bibbiyu ko uku-uku ko hurhuɗu, yana ƙara wa a cikin halitta abin da yake so". Mala'iku suna da ayyuka mabambanta, akwai masu sufuri da matsara da masu ɗaukar Al'arshi da makamantansu.

Akwai kuma littattafan Allah waɗanda suka ƙunshi maganar Allah wanzajjiya da ya saukar da ita ga Manzanninsa don su isar da ita ga bayinsa. Dukkan abubuwan da littattafan nan suka ƙunsa gaskiya ne, kuma aiki da su wajibi ne. Allah ya saukar da littattafansa kimanin ɗari da huɗu (104), su ne kuwa:

- Littattafai Sittin (60) ga Annabi Shisu
- Littattafai Talatin (30) ga Annabi Ibrahim

[18] Ba za a iya danganta Manzanni da waɗannan siffofi korarru a gare su ba.

- Littattafai Goma (10) ga Annabi Musa kafin Attaura
- Littattafai Huɗu (4): *Attaura ga Annabi Musa da Zabura* ga Annabi Dawud da *Injila* ga Annabi Isa da *Alƙur'ani* ga Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare su).

Allah, subhanahu wa ta'ala, ya ce: "Ka ce na yi imani da abin da Allah ya saukar na littafi". Haka kuma ya ce: "Lalle wannan yana daga cikiin littattafan farko, littattafan Ibrahim da Musa". Sai kuma inda Allah ya ce: "Tsarki ya tabbata ga wannan da ya saukar da abin da ke rarrabewa (*Alƙur'ani*) ga bawansa don ya zamo mai gargaɗi ga 'yan'adam".

Musulmi kuma ya yi imani da akwai wata rana da Allah zai tayar da dukkan bayinsa bayan mutuwa, a mayar musu da rayukansu. A wannan rana za a yi tsayuwa da hisabi da ma'auni da siratsi. Wannan ita ce Ranar Tashin Kiyama ko Ranar Lahira. Mutum zai ci karo ne da abin da ya aikata a duniya, ko hairi ko sharri. Za a yi hukunci bisa adalci, Allah ba zai zalunci ko ɗaya daga cikin halittarsa ba. Allah, maɗaukaki, ya ce: "Lalle sa'a mai zuwa ce babu kokonto a cikinta". Sai kuma inda ya ce, "Lalle Allah zai tayar da waɗanda ke cikin ƙaburbura".

Haka kuma duk abin da ya faru na al'amura da nufar Allah ne tun can azal. Tafiyar da al'amuran nan kuma yana kasancewa da ikonsa ne. fahimtar haka zai sa a dinga gode wa Allah da dukkan ni'imomin da ya yi wa bayinsa, da yin haƙuri a kan wani ƙunci da ya faru. Sannan a san dukkan ni'ima baiwa ce da falala, kamewa ko ƙunci adalci ne. Mutum ba shi da komi sai abin da ya tsiwurwurta da bibiyar aikin da aka ba shi damar zaɓi a kansa da zai iya zama na hairi in hairin ne ko na sharri in sharrin ne.

2

SASHEN HUKUNCE–HUKUNCEN IBADA

Musulunci mazubi ɗaya ne da yake tafiya bisa manufa ɗaya tun daga Annabi Adamu, alaihis salamu, har kawo ga Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, a matsayinsa na cikamakin Manzanni da Annabawa wanda babu wani Annabi da za a aiko a bayansa. Shi wannan addini na Musulunci, Ubangiji ya kammala shi, ya cikasa dukkan sharuɗɗansa ta hanyar Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, zuwa ga bayinsa. Allah ya gaya wa Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, addinin Musulunci ya kammalu cif a yayin da da ya yi wani hajji da ya zama na ƙarshe a gare shi wanda ake kira Hajjin Bankwana. Allah ya ce:

"*A yau na kammala muku addininku a gare ku, kuma na cika ni'imomina a kanku, sannan na yarje muku Musulunci ya zamanto addini a gare ku"* (Ma'ida, aya ta 3).

Babu tsanani a cikin addinin Musulunci, shi tsagwaron shiriya ne ga wanda ya rungume shi da hannu bibbiyu. Domin haka ne Allah yake cewa:

"*Babu tilastawa a cikin addini, haƙiƙa, shiriya ta bayyana daga ɓata, saboda haka, wanda ya kafirce wa Ɗagutu kuma ya yi imani da Allah, to, haƙiƙa, ya yi riko ga igiya (wadda take) amintacciya, babu yanke wa a*

gare ta. Kuma Allah mai ji ne, masani" (Baƙara, aya ta 256).

Bayan da Musulunci ya cika sosai, sai ya sami ginshiƙai ko shika-shikai na ibada a cikinsa har guda biyar waɗanda suka haɗa da kaɗaita Allah da Manzonsa da salla da azumi da zakka da hajji. Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabata a gare shi, ya ce: "An gina Musulunci a bisa abubuwa biyar, gaskatawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah kuma Annabi Muhammadu, bawansa ne kuma Manzonsa na ƙarshe, da tsayar da salla da yin azumin watan Ramalana da ba da zakka da aikin Hajji ga wanda ya samu iko".

Matsayin Ibada

Ibada ita ce yin ayyukan addini da gaɓoɓin jiki tare da kyautata yi a lokacin gudanar da ita da kuma neman aƙibar aikin wato a sami sakamakon ayyukan da ake aikatawa tun nan duniya da kuma gobe a lahira. Masu tsare yin ibada kuwa su ne, "Waɗanda suka tabbata lalle su masu haɗuwa ne da Ubangijinsu, kuma lalle ne su zuwa gare shi masu komawa ne" (Baƙara, aya ta 46). Shi kuma duk abin da mutum ya yi na ibada zai sami kyakkyawan sakamakonsa daga wurin Allah, kamar yadda ya ce:

"*Kuma ku tsayar da salla, kuma ku bayar da zakka. Kuma abin da kuka gabatar domin kanku daga alheri, za ku same shi a wurin Allah. Lalle ne Allah, ga abin da kuke aikatawa mai gani ne" (Baƙara, aya ta 110).*

Duk wani abu da mutum ya yi wanda aka umurce shi bisa wajabci ko ya ƙi yin aikin assha ko fasadi domin an hane shi bisa wajabci, ko ya yi wani abu na alheri domin garalin kansa,

su ne ake kira ayyukan ibada, kuma akwai sakamako bisa yin haka daga wurin Allah. Wani lokaci ma idan mutum ya lura da tasarrufinsa a cikin rayuwa duk ibada ne yake yi. Ashe ke nan gaba ɗayan rayuwar Musulmi ibada ce. Ɗauki misali da kanka, ƙafafunka ibada suke yi, haka ma guiwoyinka da cinyoyinka da al'aurarka da cikinka da zuciyarka, wadda ita ce ma turke ko ginshiƙi ko ƙashin bayan ibada, da wuyanka da bakinka da laɓɓanka da harshenka da haƙoranka da hancinka da idanunka da kunnuwanka da dukkan sassan jikinka ibada suke yi, kuma an halitta maka su don yi wa mahalincinsu ibada. Kai hatta dabbobi da itatuwa da tsirrai da duwarwatsu da gulabe da na'urorin kimiyyar zamani duk suna kan yi wa Allah ibada da bauta bisa nau'o'in hususiyyar ibadarsu zuwa ga Allah.

A wajen ɗan'adam, an neme shi ya yi wa Allah ibada don amfanin kansa da bin umurnin da aka yi masa da riƙo da shi. Daga cikin kaɗan na nau'o'in ibada akwai furta kalmar shahada da fatun baki da ƙudurcewa a zuciya, da yin salla, da yin azumi, da fitar da zakka, ta kono ko ta dukiya ko ta urula, da zuwa aikin hajji da ci da sha da sutura bisa kaifiyyarsu da aure da huldar ciniki da kasuwanci da tsayar da shugabanci da hukunci da neman ilmin saninsu da yin ihsani a cikin yin su da kyautatawa ga zangunan mutane da suka cancanta da neman lafiya da tabbatar da zama lafiya da raba gado bisa sharaɗinsa da tanajin gawa da kyauta yi a gare ta bisa cancantarta da samar da maƙabartu da gonakan neman abinci da gidajen gudanar da ibadar da muhallin zama ga mutane da makarantun neman ilmi da sauran ayyukan ibada daban-daban.

Ubangiji, mai girma da ɗaukaka ya nemi mutane su yi tsere[19] a cikin yin alheri, sannan a fuskanci alƙibla wadda za ta fitar da mutum zuwa nagartaccen gaci. Allah ya ce:

"*Kuma kowane ɓangare yana da alƙibla wadda yake shi mai fuskantarta ne. sai ku yi tsere zuwa ga ayyuukan alheri, inda kuka kasance duka, Allah zai zo da ku gaba ɗaya. Lalle ne Allah, a kan kome, mai ikon yi ne".*

"Kuma daga inda ka fita, to, sai ka juyar da fuskarka a wajen Masallaci tsararre, kuma lalle, tabbas, shi ne gaskiya daga Ubangijinka. Kuma Allah bai zama mai gafala ba daga abin da kuke aikatawa" (Baƙara, aya ta 148 – 149).

Sannan Allah, mahaliccin kowa da komi, ya yi wa mutane jagora a wajen zartar da ayyukan ibadarsu bisa riƙo da igiya ɗaya,wadda take ita ce gundarin addinin Musulunci. Yana daga cikin shika-shikan ibada, kada Musulmi su yarda su raba kawunansu. Wajibi ne gare su, su zama abu ɗaya, al'umma ɗaya a cikin tutar Musulunci wanda yin haka kuma shi ne cibiyar ibada. Allah, subhanahu wa ta'ala, yana cewa:

"*Yaku waɗanda suka yi imani! Ku bi Allah da taƙawa a kan haƙƙin bin sa da taƙawa. Kuma kada ku mutu face kuna masu sallamawa (zuwa ga Musulunci).*

"Kuma ku yi daidami da igiyar Allah gaba ɗaya kuma kada ku rarraba. Sannan ku tuna ni'imar Allah a kanku, a lokacin da kuka kasance maƙiya, sai ya sanya

[19] Wato rigengen ko gasa.

soyayya a tsakanin zukatanku, domin haka, kuka wayi gari, da ni'imarsa, 'yan'uwa. Kuma kun kasance a kan gaɓar rami na wuta, sai ya tsamar da ku daga gare ta. Kamar wannan ne Allah yake bayyana muku ayoyinsa, tsammaninku za ku shiryu" (Ali Imrana, aya ta 102 – 103).

Daga nan ne kuma Allah ya ba Musulmi dama da su tashi tsaye, tsayin daka, su dinga kiran junansu zuwa ga yin ayyuukan alheri da ƙaunar juna, don ta haka ne za a sami danƙon zama waje ɗaya. Allah ya umurce mu da cewa:

"*Kuma wata jama'a daga cikinku, su kasance suna kira zuwa ga alheri, kuma suna umurni da alheri kuma suna hani daga abin da ake ƙi. Kuma waɗannan su ne masu cin nasara" (Ali Imrana, aya ta 104).*

Wajibi ne Musulmi ya fi ƙarfin zuciyarsa, kada kuma ya sanya son zuciya a cikin aikin ibada. Bai kamata Musulmi su rarraba kawunansu ba, su mayar da Musulunci tamkar wani kanti na saye da sayarwa ko wani kamfani ko masana'anta da jagoranta kan keɓe wasu mutane su zama 'yan barandansa masu yi masa aikace-aikace don kawo masa riba daga shi sai 'ya'yansa. Shi ne Allah yake cewa kada Musulmi su saɓa da junansu bayan kuwa hujja ta zo musu ta su zama uwa ɗaya uba ɗaya:
"*Kuma kada ku kasance kamar waɗanda suka rarrabu, kuma suka saba wa juna, bayan hujjoji bayyanannu sun je musu, kuma waɗannan suna da azaba mai girma (Ali Imrana, aya ta 105).*

Allah ya bayyana sakamakon rarraba a cikin addini kamar haka:

"*Lalle ne waɗanda suka rarraba a addininsu, kuma suka kasance ƙungiya-ƙungiya, kai ba ka zama daga gare su ba, a cikin kome, abin sani kawai al'amarinsu zuwa ga Allah yake. Sannan ya ba su labari game da abin da suka kasance suna aikatawa" (An'am, aya ta 159)*.

Haƙiƙa yana da ga cikin kyawawan ayyuka mutum ya zamanto mai ƙoƙarin ƙulla zumunci a tsakanin 'yan'uwa Musulmi. Babu ruwan Allah, shi mai azabtar da mutumen da ya sani, sa'an nan ya take saninsa, kuma mai ninkawar lada ne ga mai ƙarfafa alheri:

"Wanda ya zo da kyakkyawan aiki guda to, yana da goma dîn misalansa. Kuma wanda ya zo da mugun aiki guda, to, ba za a saka masa ba face da misalinsa. Kuma su ba a zaluntarsu" (An'am, aya ta 160).

Wasu Nau'o'in Ibada a Rayuwa

Allah, subhanahu wa ta'ala, wanda ya umurci da a yi masa ibada, ya ƙarfafa wasu nau'o'in ibadu kamar haka:

Salla:

Allah yana cewa:

"*Ku tsare lokuta a kan salloli da salla mafificiya. Kuma ku tsaya kuna masu ƙanƙan da kai ga Allah" (Baƙara, aya ta 238).*

Ga yanayin da aka bayyana na salla ga Musulmi:

"Ya ku waɗanda suka yi imani! Kada ku kusanci salla alhali kuwa kuna masu maye sai kun san abin da kuke faɗa, kuma haka idan kuna masu janaba, face mai ƙetare hanya, har ku yi wanka. Kuma idan kun kasance majinyata, ko kuwa a kan tafiya, ko kuwa wani daga cikinku, idan ya zo da gayaɗi, ko kuma kun shafi mata, ba ku sami ruwa ba, to ku nufi fuskar ƙasa mai kyau, ku yi shafa ga fuskokinku da hannuwanku (wato ku yi taimama saboda rashin ruwa). Lalle ne Allah ya kasance mai yafewa mai gafara" (Nisa'i, aya ta 43).

Sallar Tsoro

Allah ya ce:

"Kuma idan kun yi tafiya a cikin ƙasa, to, babu laifi a kanku ku rage daga salla (don wani tsoro, a yi ta gwargwadon halin da ake ciki) idan kun ji tsoron waɗanda suka kafirta su fitine ku. Lalle ne kafirai sun kasance, a gare ku, maƙiyi bayyanannu" (Nisa'i, aya ta 101).

Hijira saboda Matsuwa ko Rashin Sakewa ga yin Addini

Allah ya ce:

"Kuma wanda ya yi hijira a cikin hanyar Allah, zai samu a cikin ƙasa, wuraren juyawa masu yawa da yalwa. Kuma wanda ya fita daga gidansa yana mai hijira zuwa ga Allah da Manzonsa, sa'an nan kuma mutuwa ta riske shi, to lalle ne, ladarsa ta auku ga Allah. Kuma Allah ya kasance a gare ku, mai gafara, mai jinƙai" (Nisa'i, aya ta 100).

Hajji

Allah, mai girma da ɗaukaka, ya bayyana hajji da cewa: "*Kuma akwai hajjin ɗaki domin Allah a kan mutane ga wanda ya sami ikon zuwa gare shi". (Ali Imrana, aya ta 97).*

Ubangiji ya yi umurni kada a tauye masu nufin yin hajji da wani abu na tawaya. Allah ya ce:

"Ya ku waɗanda kuka ba da gaskiya, kada ku wulaƙanta ƙa'idojin addinin Allah, kada kuma (ku wulaƙanta) wata mai alfarma (ta yin yaƙi a cikinsa), da hadaya, da kuma (hadayar da aka yi wa alama da) rataye, kada kuma ku (tare) masu nufin (ziyarar) Ɗakin Allah, suna neman falala daga Ubangijinsu da yarda". (Ma'ida, aya ta 2).

Taimakon Juna

Allah ya ce:

"Kuma ku taimaki juna a kan aikin ƙwarai[20] da taƙawa. Kuma kada ku taimaki juna a kan zunubi da zalunci[21], kuma ku bi Allah da taƙawa (ku ji tsoron Allah) (Ma'ida, aya ta 2).

Alwala

Allah ya ce:

[20] Wato ayyukan alheri da ƙarfafa yin su.

[21] Ko kuma ayyuka na saɓo. Allah ya tsare mu, amin.

"*Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kun tashi zuwa salla, to, ku wanke fuskokinku da hannuwanku zuwa ga magincirori, kuma ku yi shafa ga kunnuwanku, kuma ku (wanke) ƙafafunku, zuwa idanun sawu biyu" (Ma'ida, aya ta 6).*

Wankan Janaba

Allah ya umurci a yi wankan janaba ta cewa:
"*Kuma idan kun kasance masu janaba, to, ku yi tsarki" (Ma'ida,aya ta 6).*

Taimama

Hukuncin taimama (bugun ƙasa) ya zo a nassin *Alƙur'ani* da yake cewa:
"*Kuma idan kun kasance majinyata (marasa lafiya) ko kuwa a kan tafiya ko kuwa ɗaya daga cikinku ya zo da gayaɗi, ko kuka yi shafayyar juna da mata, sannan ba ku sami ruwa ba, to, ku yi nufin wuri mai kyau (ku yi taimama), sa'an nan ku yi shafa ga fuskokinku da hannuwanku daga gare shi. Allah ba ya nufi domin ya sanya wani ƙunci a kanku, kuma amma yana nufi domin ya cika ni'imarsa a kanku, tsammaninku kuna godewa" (Ma'ida, aya ta 6).*

Shaida da Adalci

Allah yana cewa:
"Ya ku waɗanda suka yi imani! Ku kasance masu tsayin daka domin Allah, masu shaida da adalci. Kuma kada ƙiyayya da wasu mutane ta ɗauke ku, a kan ba za ku yi adalci ba. ku yi adalci. Shi ne mafi kusa ga taƙawa. Lalle Allah masani ne ga abin da kuke aikatawa" (Ma'ida, aya ta 8).

Farautar Ruwa

Allah, maɗaukaki, ya ce:

"An halatta muku farautar ruwa da abincinsa[22], domin jin daɗi a gare ku, kuma domin matafiya" (Ma'ida, aya ta 96).

Wasu Nau'o'in Nama da aka Hana Musulmi ya ci

A nassin *Alƙur'ani* an haramta cin waɗannan nau'o'in nama. Allah yana cewa:

"An haramta muku cin mushe da jini da naman alade da abin da aka ambaci sunan wanin Allah a gare shi. da makararriya[23] da jefaffiya[24] da mai gangarowa[25] da sokakkiya[26], da abin da masu dagi suka ci, face abin da kuka yanka, da abin da aka yanka a kan gunki (shi ma an haramta shi) (Ma'ida, aya ta 3).

Sallar Juma'a

Allah ya ce:

"Ya ku waɗanda suka yi imani, idan an yi kira zuwa ga salla a ranar Juma'a, sai ku yi gaugawa zuwa ga ambaton Allah, kuma ku bar ciniki. Wancan ɗinku ne mafi alheri a gare ku idan kun kasance kuna sani" (Juma'a, aya ta 9).

Neman Falalar Allah[27]

Allah yana cewa:

---

[22] Wato abincin da kogi ya yi ambaliyarsa.
[23] Wato dabba wadda aka shaƙe.
[24] Wato dabba wadda aka jefa ta mutu.
[25] Wato dabba wadda ta gangaro daga saman wani abu ta mutu.
[26] Wato dabba wadda 'yar'uwarta ta soke da ƙaho ta mutu.
[27] Wato abubuwan tallafin zamar rayuwa.

“Sannan idan an ƙare salla, sai ku watsu (fantsama) a cikin ƙasa kuma ku nema daga falalar Allah, kuma ku ambaci sunan Allah da yawa,tsammaninku, ku sami babban rabo” (Juma’a, aya ta 10).

Zakka

Allah ya ce:

“Ka riƙi sadaka daga dukiyoyinsu don ta tsarkake su kuma ta tsaftace rayukansu da ita”.

Akwai kuma:

“kuma ku tsayar da salla; kuma ku bayar da zakka; kuma ku yi ruku’i tare da masu yin ruku’i (Baƙara, aya ta 43).

Akwai kuma:

‘Lalle dukiyoyin sadaka na faƙirai ne da miskinai da masu aiki a kansu da waɗanda ake lallashin zukatansu, kuma da a cikin fansar wuyoyi da mabarta da a cikin hanyar Allah da ɗan hanya (matafiyi, farilla daga Allah, kuma Allah ne masani mai hikima (Tauba, aya ta 60).

Azumi

Allah yana faɗin:

“Ya ku waɗanda suka yi imani! An wajabta muku yin azumi kamar yadda aka wajabta wa waɗannan da suka gabace ku, ko la’alla za ku ji tsoron Allah (tsammaninku, za ku yi taƙawa)” (Baƙara, aya ta 183).

Yin Aure

Allah ya ce:

“Ku auri abin da ya yi muku daɗi daga, biyu – biyu, ko uku-uku ko huɗu-huɗu. Idan kuma kun ji tsoron ba za

ku yi adalci ba, to, (ku auri) guda ɗaya ko kuwa abin da hannuwanku na dama suka mallaka. Wannan shi ne mafi kusantar zama ba ku wuce haddi ba"(Nisa'i,aya ta 3).

Gado

Allah yana cewa:

"Kuma an wajabta a kanku, idan mutuwa ta halarci ɗayaku idan ya bar wata dukiya, wasiyya domin mahaifa da dangi bisa ga abin da aka sani, wajabce a kan masu taƙawa" (Baƙara, ayata 180).

Dukkan maza da mata ne masu yin gadon Mamaci

Allah yana cewa:

"Maza suna da rabo daga abin da iyaye biyu (uba da uwa) da mafi kusantar dangi suka (rasu suka) bari, kuma mata suna da rabo daga abin da iyaye biyu (uba da uwa) da mafi kusantar dangi suka (rasu suka) bari, daga abin da ya ƙaranta daga gare shi ko kuma ya yi yawa, rabo yankakke" (Nisa'i,aya ta 7).

Rayuwar Duniya da Mutuwa da Aljanna da Wuta

Allah ya ce:

"Kowane rai mai ɗanɗanar mutuwa ne. kuma ana cika muku ijarorinku kawai ne a Ranar Kiyama. To, wanda aka nisantar daga barin wuta, kuma aka shigar da shi Aljanna, to, lalle ne ya tsira. Kuma rayuwar duniya ba ta zama ba face jin daɗin ruɗi" (Ali Imrana, aya ta 185).

Kashe Rai

Allah yana faɗin:

"Kuma kada ku kashe rai wanda Allah ya haramta face da haƙƙi, kuma wanda aka kashe, yana wanda aka zalunta, to, haƙiƙa, mun sanya hujja ga waliyinsa, sai dai kada ya ƙetare haddi a cikin kashewar[28]. Lalle shi ya kasance wanda ake taimako" (Isra'i, aya ta 33).

Dukiyar Maraya

Allah ya ce:

"Kuma kada ku kusanci dukiyar maraya face sai da siffa wadda take ita ce mafi kyau, har ya isa ga mafi ƙarfinsa kuma ku cika alƙawari. Lalle alƙawari ya kasance abin tambayawa ne" (Isra'i, aya ta 34).

Cika Ma'auni da Sikeli Madaidaici

Allah ya ce:

"Kuma ku cika mudu idan kun yi awo, kuma ku auna nauyi da sikeli madaidaici. Wancan ne mafi alheri, kuma mafi kyau ga fassara[29]" (Isra'i, aya ta 35).

Yin Aiki da Ilmi da Tafiya Cikin Nutsuwa

Allah yana cewa:

"Kuma kada ka bi abin da ba ka da ilmi game da shi. Lalle ne ji da gani da zuciya, dukan waɗancan (mutum) ya kasance daga gare shi wanda ake tambaya".

---

[28] Wato magajin wanda aka kashe yana da damar ya nemi ramuwa amma kada a ƙetare iyaka.

[29] Cika ma'auni shi ne cikar adalci kuma ta yin haka dukiya za ta yi albarka, za a kuma sami kyakkyawan ƙarshe. Shi kuma tauye ma'auni mummunan aiki ne.

"Kuma kada ka yi tafiya a cikin ƙasa da alfahari. Lalle kai, ba za ka huda ƙasa ba, kuma ba za ka kai ga duwatsu ba ga tsawo" (Isra'i, aya ta 36 – 37).

Nisantar Zina

Allah yana cewa:

"Kuma kada ku kusanci zina. Lalle ne ita ta kasance alfasha ce kuma ta munana ga zama hanya" (Isra'i, ayata 32).

Kashe 'Ya'ya Saboda Talauci

Allah yana cewa:

"Kuma kada ku kashe 'ya'yanku domin tsoron talauci. Mu ne ke azurta su, su da ku. Lalle ne kashe su ya kasance kuskure babba" (Isra'i, aya ta 31)

Kyauta yi ga Abokan Zama

Allah yana cewa:

"Kuma ka bai wa ma'abocin zumunta (da maƙwabtaka) haƙkinsa (haƙkin zumu shi ne alheri da sadar da zumunta), da miskinai da ɗan hanya (ta ba su zakka da sadakar taɗauwu'i da liyafar kwana uku ga baƙo bisa ƙarfin iko ba tilastawa). Kuma kada ka bazzara dukiyarka, bazzararwa[30]" (Isra'i, aya ta 26).

Kayutata wa Iyaye

[30] Wato a kashe kuɗi ba bisa ƙa'ida ba, ko kuma ba bisa wani aiki mai kyau ba, ko wuce gona da iri a wajen kashe kuɗi.

Allah ya ce:

“Kuma Ubangijinka ya hukunta kada ku bauta wa kowa face shi, kuma game da mahaifa biyu (Uba da Uwa) ku kyautata, kyautatawa, ko dai ɗayansu ya kai ga tsufa a wurinka ko dukkansu biyu, to,kada ka ce musu tir kuma kada ka tsawace su, kuma ka faɗa musu magana mai karimci. Kuma ka sassauta musu fikafikan tausasawa na rahama. Kuma ka ce, “Ya Ubangijina! Ka yi musu rahama, kamar yadda suka yi renona, ina ƙarami” (Isra’i, aya ta 23-24).

Wa’azi

Allah ya ce, game da yin wa’azi:

“Ka yi kira zuwa ga hanyar Ubangijinka da hikima da wa’azi mai kyau, kuma ka yi jayayya da su da magana wadda take mafi kyau. Lalle ne Ubangijinka shi ne mafi sani ga wanda ya ɓace daga hanyarsa, kuma shi ne mafi sani ga masu shiryuwa” (Nahli, aya ta 125).

Zaɓin kai Bisa Aikin yi

Mutum yana da damar yin zaɓi kan aikin da zai yi. Dubi abin da Allah yake cewa:

“Wanda ya nemi shiryarwa, to ya nemi shiryuwa ne domin kansa kawai kuma wanda ya ɓace, to, ya ɓace ne a kansa kawai, kuma rai mai ɗaukar nauyi, ba ya ɗaukar nauyin wani ran, kuma ba mu zama masu yin azaba ba, sai mun aika wani Manzo”[31] *(Isra’i, aya ta 15).*

[31] Manzo wanda zai bayyana saƙon Allahu dangane da *yi* ko *bari*. Idan mutum ya sami ilimin haka zai zaɓi abin da zai kai shi gaci.

Waɗannan kaɗan ke nan daga cikin abubuwan ibada da ake son mutum ya yi ko ya bari, sannan kuma ya kyautata a cikin yin aikin nasa. Allah, tabaraka wa ta'ala, ya umurci bayinsa da su yi ayyukan alheri, su nisanci ayyukan ɓarna, marasa kyau. Allah ya yi umurni da kwaɗaitarwa a kan aikata ayyuka na ƙwarai, kamar waɗannan da suka fito a cikin nassin *Alƙur'ani* mai girma:

"Lalle Allah na yin umurni da adalci da kyautatawa, da ba wa ma'abocin zumunta, kuma yana hani ga alfasha da abin da ake ƙi da rarrabe jama'a. Yana yi muku gargaɗi ɗammaninku, kuna tunawa. Kuma ku cika da alƙawarin Allah idan kun yi alƙawari, kuma kada ku warware rantsuwoyinku a bayan ƙarfafa su alhali kuma haƙiƙa kun sanya Allah mai lamuncewa a kanku. Kuma lalle, Allah ne yake sanin abin da kuke aikatawa" (Suratul –Nahli, aya ta 90 – 91).

Alwala da Yadda ake yin ta

Alwala tsarki ne na ruwa da aka danganta shi da wasu ayyanannun gaɓoɓi na jikin mutum tare da kyautace yin niyya. Alwala tana sa mai ibada ya zama mai tsarki da zai ba shi damar kusantar Ubangijinsa cikin hali da yanayi mai kyau. Ana buƙatar mai alwala ya yi waɗannan abubuwa kafin da lokacin da yake yin alwalarsa:

- Aswaki da itacen da ya dace, ko yatsa na dama ko burushi na zamani.

- Tsarkin jiki a gusar da dukan najasa daga jiki kamar fitsari da kashi da janaba da haila da jinin biƙi da sauransu[32].

- Kyautace yin niyya cewa za a yi alwala ne don ibada. Yin niyya a kowane aiki na ibada farilla ne.

- Ana farawa ne da gaɓoɓin dama zuwa ga na hagu.

- Ba a son a yi magana a lokacin alwala, sai bisa lalura.

- Kwaryar ruwa ko kwano da ke a buɗe, za a aje su a hannun dama ne, idan buta ce rufaffiya, sai a aje ta a hagu.

- Ba a son ƙari bisa abin da aka shar'anta na wanke gaɓoɓi sau uku ko sau ɗaya.

- Cuɗanyawa da gaggautawa da jerantawa farilla ne a cikin ayyukan alwala.

- A lokacin fara alwala sai a ce: *Bismillahir rahmanir rahim.* Yin Bismilla mustahabbi ne.

Bayan an tabatar da waɗannan sai a shiga cikin alwala bisa siffofinta da jerantawar wanke gaɓoɓi kamar haka:

i. Za a fara wanke yatsu da tafukan hannuwa ciki da waje zuwa wuyansu, a kuma tsettsefe su har sau uku, amma tun kafin a shigar da su cikin ƙwaryar[33] alwala. Yin wannan aiki sunna ne. a lokacin da ake wanke hannuwa, sai a ce: *Nawaitu Sunanul Wudu'i.*

---

[32] Ana so mutum ya zama mai tsarki kafin ya fara alwalarsa, ya zama babu wata najasa ta hadasi ko hubushi a jikinsa.

[33] Wato mazubin ruwa na alwala wanda yake a buɗe ba a rufe ba.

ii. Kurkure baki inda za a shigar da ruwa a baki ana Kurkurewa ana zubarwa sau uku. Yin haka ma sunna ne.

iii. Shaƙa ruwa a cikin hanci da fyacewa sau uku. Za a shaƙa ruwa da cikin tafin hannun dama, a fyace ta riƙe hanci da farce (ɗan'yatsa) babba da manuni na hannun hagu. Yin haka sunna ne.

iv. Wanke dukkan iyakar fuska daga matsirar gashin kai, zuwa ƙarshen haɓa, sannan da tsakanin kunnuwa biyu daga dama zuwa hagu. Za a wanke kowane lungu na fuska da wuraren takurarta, da tsefe gemu. Yin haka farilla ne: Lokacin da aka zo wanke fuska sai a ce: *Nawaitu Fara'ilar Wudu'i.*

v. Wanke hannuwa zuwa guiwa na dama da na hagu da tsettsefe yatsun hannuwa sau uku. Yin haka ma farilla ne.

vi. Shafar kai tun daga farkon fuska wato matsirar gashi zuwa ƙeya farilla ne. shi ko mayar da shafar kai daga ƙeya zuwa goshi sunna ne.

vii. Shafar kunnuwa da ƙwalƙwale dukan dattinsu cikinsu da wajensu ta hanyar amfani da farce

manuni da babban yatsa. Yin haka sunna ne.

viii. Wanke ƙafafuwa zuwa idon sawu, tare da kyautace yin wannan aiki sau uku. Yin haka farilla ne.

ix. Alwala ta gamu ke nan sai yin addu'a. An so a ce:

Ash-hadu an La'ilaha illallahu, Wahdahu lasharika lahu, wa ash-hadu anna Muhammadan abduhu wa rasuluhu. Allahumma Ij'alni minat tauwabina, waj'alni minal-mutaɗahhirina, waj'alni min ibadikas salihina, waj'alni minhum ya Rabal-Alamina.

Salloli na Farilla

Salla ta farilla ita ce aka tilasta yin ta ga dukkan Musulmi mazansu da matansu, balagaggu, masu hankali da sharuɗɗan Musulunci suka rataya a kansu. Duk wanda ya yi imani da Allah da Manzonsa, an umurce shi da yin salla. Kin yin salla ga mutum Musulmi ko daina yin ta, ko yi ana hutawa, ko ƙin yin ta bisa yanayinta, dukkan ɗayan waɗannan abubuwa suna cikin manyan laifuka, ga zunubi kuma da za a iya ladabtarwa a kan haka.

Salloli na Farilla guda biyar ne, su ne kamar haka:

Salla ta ɗaya: Sallar Subahin, mai raka'a biyu
Salla ta biyu: Sallar Azahar, mai raka'a huɗu
Salla ta uku: Sallar La'asar, mai raka'a huɗu
Salla ta huɗu: Sallar Magriba, mai raka'a uku
Salla ta biyar: Sallar Isha'i mai raka'a huɗu

Salloli na Nafila

Salla ta Nafila raka'o'i ne da ake son mutum Musulmi ya dinga yi a matsayin sunna ko mustahabi waɗanda aka lura Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, yana yin su kafin salla ta farilla ko bayanta, ko a wasu lokuta na musamman, kamar Kiyamul-Laili, salloli na rayar da dare; da salloli na rayar da hantsi da ake kira Sallar Luha da sauransu. Sallar Nafila ba wajiba ce ba, salla ce ta neman ƙarin lada daga wurin Allah. Akwai lada mai yawa ga aikata ta, amman babu zunubi ga barinta, sai dai an bar aiki mai kyau. Sallar Nafila na iya zama nau'i uku:

i. Sunna mai Ƙarfi

Sallolin nafila a matsayin sunna mai ƙarfi, su ne sallolin da Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ba da ƙarfi sosai wajen yin su, kafin da bayan salloli na farilla.

ii. Suna ba mai Ƙarfi ba[34]

Sallolin nafila na sunna ba mai ƙarfi ba, salloli ne da Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, yake aikatawa bisa fashi daga lokaci zuwa lokaci.

iii. Nafila ta Musamman

Nafila ta musamman ita ce ake yi don neman ƙarin yardar Allah da ƙarin lada. Ana yin ta a lokaci natsattse, na musamman wanda ya dace kamar da dare ko da hantsi.

[34] Sunna abar zaɓi wadda ake yi ba a ko da yaushe ba.

Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, yana kwaɗaitar da yin irin waɗannan salloli na nafila.

Nafilolin da ake so a yi kafin da bayan salla ta farilla su ne:

- Raka'a biyu kafin salla ta Subahin wato su ne Raka'atal Fajri.

- Raka'a biyu ko huɗu kafin sallar Azahar, da raka'a biyu bayanta bisa taƙaitawa, amma ana iya yi yadda ake da lokaci.

- Raka'a biyu ko huɗu kafin sallar La'asar. Aliyu ɗan Abiɗalib, radiyallahu anhu, ya ce: Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya kasance yakan yi raka'a huɗu ya raba su bibbiyu da sallama kafin sallar La'asar.

- Raka'a biyu bayan sallar Magriba bisa taƙaitawa, amma ana iya yin fiye da haka. Wasu sukan yi raka'a biyu gab da Muhtarin Magriba, saboda ruwayar Abdullahi ɗan Mughaffal wanda ya bayyana Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce: 'ku yi nafila kafin sallar Magriba'.

- Raka'o'i da ba su da adadi gwagwadon lokaci kafin sallar Isha'i da raka'a biyu, sunna mai ƙarfi, bayanta da wasu nafiloli ƙari gwargwadon yadda ake da lokaci.

- Sai a sallaci shafa'i raka'a biyu da witiri raka'a ɗaya. Shafa'i da wutiri sunna ne mai ƙarfi da Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ƙarfafa yin su a ko da yaushe. Amma an fi son a sallaci raka'ar wutiri a ƙarshen sallolin dare.

Lokutan Salla

Lokacin salla shi ne ƙayyadajjen waƙati da aka sharɗanta yin ibada a cikinsa.
Kowace salla ta farilla tana da lokuta guda biyu:

- Lokaci Muhtari (zaɓaɓɓe)

- Lokaci Laluri (bisa lalura)

i. Zaɓaɓɓen lokaci na sallar Azahar yana farawa daga karkatar rana daga tsakiyar sama wato zauwali, ya ƙare ƙarshen ƙama (kamu guda na tsayuwar mutum).

Lalurinta: Daga farkon Muhtari na La'asar zuwa gab da fatsi-fatsin rana.

ii. Zaɓaɓɓen lokaci na sallar La'asar yana farawa daga kamu guda na tsayuwar mutum, ya ƙare a lokacin da rana ta yi fatsi-fatsi.

Lalurinta: daga tsakanin ja-jan rana zuwa faɗuwarta.

iii. Zaɓaɓɓen lokaci na sallar Magriba yana shiga ne a lokacin da rana ta yi ja-ja zuwa faɗuwa. Lokaci ne gajere da zai ishi a yi sallar Magriba kawai.

Lalurinta: Daga ƙare sallarta zuwa ɓullowar Alfijir.

iv. Zaɓaɓɓen lokaci na sallar Isha'i yana farawa daga ɓacewar ja-jan rana har zuwa sulusin farko na dare.

Lalurinta: Daga ƙashen kashin farko na ɗaya bisa ukun dare zuwa ketowar Alfijir.

v. Zaɓaɓɓen lokaci na sallar Subahin yana shiga ne daga hudowar Alfijir zuwa wayewar safiya ta yadda mutum zai iya gane ɗan'uwansa.

Lalurinta: Daga wayewar safiya zuwa ɓullowar rana.

Salla da Shirya Mata

Salla tana cikin shika-shikan Musulunci guda biyar. Ita ce ta biyu bayan kalmar shahada. Salla na daga cikin abubuwa biyar da suka haɗu suka gina Musulunci, domin haka, salla wajiba[35] ce ga dukkan Musulmi.

Salla ta wajabta ga dukkan namiji da mace, baligi ko baliga, masu hankali da sharuɗɗan Musulunci suka rataya a kansu.

Wanda ya ƙi yin salla, sai a umurce shi da yin ta har kwana uku idan ya musanta, sai a halatta jininsa. Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce, "Jinin mutum Musulmi ba ya halatta, sai da ɗayan abubuwan nan uku: Bazawari, mazinaci, da rai a bakin rai; da wanda ya bar addininsa ya ware kansa daga jama'a (Buhari da Muslim ne suka ruwaito shi).

Ana son wanda zai yi salla ya fara aikata waɗannan abubuwa:

- Tsarkake jiki daga dukkan najasa.
- Tufafin da za a yi salla da su, su kasance masu tsarki masu tsafta.
- Bagiren da za a yi salla ya kasance mai tsarki, ba mai najasa ba, keɓantacce wanda shari'a ta yarda da shi.

[35] Wato wajabci na farlu ainun, dole ne kowane Musulmi ya yi salla, kuma salla ba ta faɗuwa, ana rama ta idan lalura ta sanya ba a yi ta ba.

- Yin alwala a lokacin lafiya, ko yin taimama a lokacin kamuwa da wata lalura.

- Kudurce sallar da za a yi a rai.

- Kiyaye lokacinta muhtari, sai bisa lalura.

Allah, mai girma da ɗaukaka, ya sanya dukkan ƙasa wurin salla ga Musulmi, muddin dai ɗan'adam bai juya mata hali ko kama ba. An fi son a gina masallatai, a dinga salla a cikinsu, don haka aka yi umurni bisa samun haɗuwar kan Musulmi. An rangwanta ga 'ya mace Musulma ta yi salla a ɗakinta, ko da yake tsofaffi mata na iya zuwa Masallaci, su tsaya a keɓaɓɓen wurinsu da aka ware musu.
Samun waɗannan abubuwa shi ne tabbacin an shirya wa yin salla, sai a fuskanci gabas wato Alƙibla, a tsaya bisa nutsuwa. Idan sallar jam'i ce, bayan an yi Azanu wato kiran salla, sai a daidaita sahu sosai. Sannan a ta da Iƙama, a yi niyyar sallar da za a yi bisa lokacinta, sai a yi wannan salla bisa raka'o'inta ayyanannu, ko sallar Azahar ko La'asar ko Magriba, ko Isha'i ko Subahin wato dai ɗayan waɗannan salloli guda biyar na farilla.

Siffar Salla
Idan mutum ya tashi zai yi salla zai fara gabatar da tsarki na jikinsa da tufafinsa da muhallin da zai yi sallar ne. Sai kuma ya yi alwala, tare da yin aswaki kafin a shiga cikin alwala kamar yadda bayani ya gabata. Ana yin salla ne bisa lokacinta da yanayinta, wato salla ta farilla ko nafila. Ana son a yi salla a cikin jam'i kuma a Masallaci, musamman ga mutum namiji,

amma babu laifi idan tsofaffin mata sun tafi Masallaci. Kiran salla a lokacin da za a yi salla abu ne da addini ya ƙarfafa yin sa a daura da lokacin kowace salla ta farilla. Wannan shi ne bayanin siffar salla wato yadda za a yi ta bisa kaifiyyarta:

Abin da za a fara yi na shiga salla shi ne yin Azanu da iƙama:

Lafazin Kira Sallah shi ne:

Allahu Akbar,
Allahu Akbar.ɗ2

Ash-hadu alla ilaha illallah,
Ash-hadu alla ilaha illallah. ɗ2

Ash-hadu anna Muhammadar Rasulullah,
Ash-hadu anna Muhammadar Rasulullah. ɗ2

Hayya alas salat,
Hayya alas salat. ɗ2

Hayya alal falah,
Hayya alal falah. ɗ2

Allahu Akbar,
Allahu Akbar.

La'ilaha illallah[36].

[36] An fi so a yi kiran salla a wajen masallaci domin a jiyo ladan daidai-wa-daida. Kuma a lokacin kiran salla ana so mu'azzinu ya dinga jujjuya fuskarsa dama da hauni, shi ma domin ya jiyar da mutane sosai da sosai ta kowane gefe. Kuma ana so ladan ya dinga ɗaukaka murya a wuraren maimaita lafuzzan kiran salla.

Lafazin Iƙama shi ne:
Allahu Akar,
Allahu Akar,
Ash hadu an la'ilaha illallah,
Ash hadu anna Muhammadar Rasulullah
Hayya alas salah,
Hayya alal falah,
Ƙad ƙamatis salah,
Allahu Akbar,
Allahu Akbar,
La'ilaha illallah.

A lokacin da ake wannan iƙama an riga an daidaita sahu ana daɗa kintsawa tare da fuskantar alƙibla wato Ka'aba ko Ɗakin Allah.
Sai a yi niyyar yin ayyananniyar sallar da aka nufata wato subahin ko Azahar ko La'asar ko Magriba ko Isha'i ko sallar nafila. Ana yin niyya a cikin zuciya ne tare da ƙudurcewa. Alalmisali, idan sallar Magriba ce, sai a ce: "Na yi niyyar sallar Magriba ta farilla" (*Nawaitu salatal Magrib farlun* ko *Nawaitu Iƙtida'a bil-Imami fi salatil Magrib*).
Da an gama ƙudurce niyya, sai a yi kabbarar harama, a ce: *Allahu Akbar*, ana mai ɗaga hannuwa zuwa sama daura da kafaɗun mai yin salla. *Allahu Akbar* ta farko ita ce ake kira Kabbarar Harama, yin ta tare da niyya farilla ne a cikin salla.
Za a tsayu bisa daidaito, ƙyam, cikin nutsuwa, wasu suna kame da hannuwansu ne daura da ƙirjinsu (a yi ƙablu), wasu kuma suna sakin hannuwansu a ƙasa ne, suna reto (a yi sadalu), kuma kowannensu da hujjojinsa na yin haka.
Daga nan tsaye za a karanci fatiha da wani abu da ya sauƙaƙa daga cikin ayoyi ko surorin *Alƙur'ani*. A wajen karatu na wasu salloli ana yin sa ne a bayyane wato kamar a sallar *Subahin* da

Magriba da *Isha'i*, wasu sallolin kuma ana yin sa a ɓoye wato kamar sallar *Azahar* da *La'asar*.

Bayan an gama karatun *fatiha* da *sura* sai a yi *ruku'i*, ana cewa *Subhana Rabbiyal Azim wa Bihamdihi* ko *Subhanakal Lahumma Rabana wa Bihamdika, Allahumma igfirli* (Buhari da Muslim suka ruwaito haka). A lokacin da za a surmuya zuwa ruku'i sai a ce *Allahumma Rabbana wa lakal hamd* ko a taƙaice *Rabbana wa lakal hamd*. Ko kuma *Rabbana wa lakal hamd, hamdan kasiran ɗayyiban mubarakan fihi*. Sai kuma a ɗaukako daga ruku'i, ana mai tasowa sama da cewa: *Sami'allahu liman hamidah*. A wajen yin ruku'i ana son a duƙa sosai a daidatu ta yadda ko da an ɗora ƙwarya a bayan mutum za ta tsaya, ba a yi ƙasa ko a yi sama ba.

Ana daga nan tsaye, tsayuwa madaidaiciya. Sai a surmuyo zuwa yin sujadar farko domin sujada (kai goshi ƙasa) a kowace raka'a guda biyu ce ake yi. Lokacin da ake surmuyowa za a tafo da cewa *Allahu Akbar*. Ana son lokacin da za a ƙare furta *Akbar* an kai goshi ƙasa. Za a sanya hannuwa guda biyu (dama da hagu) a tsakanin kunnuwan mutum, a shimfiɗa tafunansu daidai bisa ga ƙasa, kuma su daidaitu sosai. Sannan sai a ce, *Subhana Rabbiyal A'ala wa bi Hamdih*i. A wannan lokacin an ba mai yin sujada damar ya yi addu'ar da yake so gwargwadon bukatarsa. Musulmi ya ruwaito cewa, Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya kasance yana faɗi a yayin sujada:

"Allahummagfirli zambi kullahu, diƙƙahu, wa jillahu, auwalahu wa ahirahu wa alaniyyatahu wa sirrahu (Ruwayar Muslim).

Sai a ɗaukako kai daga sujada, a kuma zauna ba mai tsawo ba (shi ne ake kira zama na tsakanin sujadu guda biyu). A lokacin da ake zaune an so a ce:

"*Allahum magfirli warhamni wahdini wahdi abna'i wa'afu anni, warzuƙni wajburni warfa'ani* :(Abu Dawud ya rawaito haka).

Daga nan sai a sake surmuyawa a je a yi sujada ta biyu ana mai cewa *Allah Akbar*. A kuma maimaita duk abin da aka yi a sujada ta farko na aiki da addu'a. Sai kuma a ɗaukaka kai zuwa ga raka'a ta biyu[37].
Idan an kawo raka'a ta biyu kamar yadda aka yi ta farko da tsayuwar karatun fatiha da sura da ruku'i da sujadu, sai a zauna a yi tahiya. Zaman tahiya guda ɗaya ne ga sallar Subahin wadda ke da raka'a biyu kawai, amma sau biyu ake yin sa ga sallolin Magriba da Isha'i da Azahar da La'asar masu raka'o'i uku da hurhuɗu. A wajen waɗannan salloli akwai zama na biyu wanda bayan an yi tahiya za a yi sallamar ƙare salla, shi kuma yin sa farilla ne.
Lafazin tahiya shi ne:

"Attahiyayatu lillahi, Azzakiyatu lillahi, Aɗɗayyibatus Salawatu Lillahi. Assalamu alaika ayyuhan Nabiyyu wa rahmatullahi ta'ala wa Barakatuhu. Assalamu alaina wa ala ibadillahis Salihina. Ash hadu an La'ilaha illallahu, wa ash hadu anna Muhammadan abduhu wa rasuluhu".

[37] Wasu kafin su miƙe zuwa ga raka'a ta biyu, suna yin zama kaɗan, kamar wanda ake yi a tsakanin sujadu biyu, don a huta. Su ma masu yin haka suna da madogara daga sunna.

Ga salloli masu raka'o'i uku (Magriba) da hurhuɗu (Isha'i, Azahar, La'asar) idan an tashi za a kawo raka'a ta uku ko ta huɗu za a karanci fatiha ne kawai, sannan a je a yi ruku'i da sujadu guda biyu.

A wajen zaman ƙarshe bayan an karanta tahiya (Tashahhudu), an so mai yin salla ya yi addu'a inda zai fara da salati ga Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, sannan ya roƙi gafarar Allah. Ga misali:

Allahumma salli ala Muhammadin wa ala ali Muhammadin kama sallaita ala Ibrahim wa ala ali Ibrahim, innaka hamidun majid. Allahumma barik ala Muhammadin wa ala ali Muhammadin, kama barakta ala Ibrahim, wa ala ali Ibrahim, innaka hamidun majid.

Ga misalin wata addu'a bayan salatin Ibrahimiyya:

Allahumma inni zalamtu nafsi zulman kasiran, wala yagfiruz zunuba illa anta. Fagfirli, magfiratan min indika warhamni, innaka antal gafurul rahim (Daga Buhari da Muslim).

Ko kuma:

Allahumma inni as'alukas sabatu fil- amri, wal-azimata alal-rushdi, wa as'aluka shukra ni'imatika wa husna ibadatika, wa as'aluka ƙalban saliman, walisanan sadiƙan, wa as'aluka min hairi ma ta'alamu, wa a'uzu bika min sharri ma ta'alamu, wa astagfiruka lima ta'alamu (Ruwayar Nisa'i).

Ko kuma:

Allahumma inni a'uzu bika min azabil-ƙabri, wa a'uzu bika min fitnatid dajjal, wa a'uzu bika min fitnatil-mahaya, wal mamati. Allahumma inni a'uzu bika minal ma'asami wal magrami" (Daga Ruwayar Buhari da Muslim).

Akwai kuma:

Rabbi ij'alni muƙimas salati wa min zurriyyati, Rabbana wa taƙabbal du'a'i. Rabanagfirli wa liwalidayya wa lilmuminina yauma ya ƙumul-hisab".

Sallamar Fitar Salla

Bayan Masallaci ya ƙare yin addu'a gwargwadon ƙarfinsa da ikonsa, sai ya yi sallama, ya ce, *Assalamu Alaikum wa rahmatullah*. Wannan kuma ita ce ake kira *Sallamar Fitar Salla.*

A lokacin da mutum yake yin sallama zai dinga karkata fuskarsa a hankali ta sashen damarsa, yana ƙara cewa "Warahmatullah" fuskarsa ta kai daura da kafaɗarsa. Sannan kuma ya juyo, ya yi haka a hagunsa. A Malikiyya idan mutum yana salla tare da liman ne, bayan liman ya yi sallama kamar yadda aka bayyana a baya, sai shi ya yi sallama ta farko a damarsa, sannan ya dubi gabansa, daura da liman ya yi masa sallama, idan akwai wani mutum a hagunsa, shi ma sai ya yi masa sallama. Shi ke nan salla ta ƙare mai raka'a biyu (Subahin ko uku (Magriba) ko hurhuɗu (Isha'i da Azahar da La'asar).

Bayan an gama salla, kafin mutum ya tashi zuwa ga harkokinsa na yau da kullum, an so matuƙa ya dakata, ya ƙara

yin addu'a, musamman tasbihi inda zai ce *Subhanallahi* sau talatin da uku (33) *Walhamdu lillahi* sau talatin da uku (33) *Wallahu Akbar* sau talatin da uku (33). Ya cikasa ɗari da cewa *Ash hadu an la'ilaha illallahu wahdahu lasharika lahu wa ash hadu anna Muhammadan abduhu wa rasuluhu.*
Sannan mutum ya shiga yin addu'o'in da suka sauƙaƙa a gare shi.

Salloli na Farilla da Bishiyarsu
Ana iya taƙaita salloli na farilla a tsarin bishiya kamar haka:

Sallar Subahin (Raka'o'i Biyu)



Sallar Azahar (Raka'o'i Huɗu)



Zama na biyu + Tahiya + Sallama

Sallar La'asar (Raka'o'i Huɗu)



Sallar Magrib (Raka'o'i Uku)



Sallar Isha'i (Raka'o'i Huɗu)



Sallolin Nafila
Wasu daga cikin sallolin da ake yi na nafila da ba na farilla ba akwai:

- Sallar Tarawihi (Alkareji) a watan Azumi=Bisa ƙaranci, Raka'o'i goma da sallama biyar ne ake yi, ko raka'o'i takwas da sallama huɗu a bayan duk raka'o'i biyu.
- Shafa'i=Raka'o'i biyu
- Witir=Raka'a ɗaya=ana yin sa a ƙarshen dare kafin ketowar alfijir.
- Sallar Idil Fiɗiri=Raka'o'i biyu
- Sallar Idil Kabir=Raka'o'i biyu
- Sallar Kisfewar Wata=Raka'o'i aƙalla guda biyu.
- Sallar Jana'iza=Raka'o'i huɗu da ake rarrabewa da kabbarori, ba a yin ruku'i ko sujada. Daga tsaye ake yin ta ba a duƙawa.
- Sallar Roƙon Ruwa=Raka'o'i guda biyu.
- da sauransu.

Farillan Salla
Shigar lokacin salla

Tsarki

Niyya

Kabbarar Harama

Tsayuwa ga yin Kabbara

Kartun Fatiha

Tsayuwa ga Karatun Fatiha

Ruku'i

Ɗaukakowa daga Ruku'i

Sujada

Ɗaukakowa daga Sujada

Zama na Biyu ta yadda za a yi sallama

Daidaito

Nutsuwa

Sallamar Fitar salla

Rashin yin zance sai da lalura

Sunnonin Salla

Ɗaga hannuwa a wajen Kabarar Harama

Karatun sura bayan fatiha

Tsayuwa ga karatun sura

Zama na farko

Karatun Tahiya

Kabbara ta zuwa zama

Damantawa da kai zuwa kafaɗa a yayin sallama

Bayyana karatun da ake bayyanawa

Sirranta karatun da ake sirrantawa

Faɗin *Sami'allahu liman Hamidahu*

Yin sallama ta gefen dama

Yin sallama ta gefen hagu (in da akwai mutum)

Yin sallama ga Liman (Idan sallar jam'i ce kuma a Malikiyya).

Mustahabban Salla

Sirrantawar Mamu, a yayin sirratawar Liman

Tsawaita karatu a sallar Subahin da Azahar

Taƙaita karatu a sallar La'asar da Magriba

Tsakaitawar karatu a sallar Isha'i

Yin Tasbihi a lokacin ruku'i

Yin addu'a a lokacin sujada

Karanta Alƙunuti

Zaman tahiya bisa ƙafa ta hagu

Ɗora hannuwa bisa cinyoyi

Miƙar da yatsa manuni a tsaye kawai ko motsar da shi

Abubuwan da ke Ɓata Salla

Rashin alwala ko taimama

Rashin fuskantar alƙibla da gangan

Zance da gangan ba da mantuwa ba

Yin salla kafin lokacinta

Yin dariya

Yin ayyuka masu yawa

Kamuwa da najasa

Yayewar al'aura

Cin abinci ko abin sha a cikin salla

Maimaita salla bisa yawan raka'o'inta

Lalurar da ke sa a yi Ba'adi a Salla
Sujada Ba'adi, sujadu ne guda biyu da ake yi bayan an yi sallama saboda wani ƙari da aka yi a cikin salla, kamar haka:

Magana da mantuwa

Sallame salla ba tare da ta ƙare ba

Karin raka'a a cikin salla, muddin dai ba a yi kamar yawan raka'o'inta ba

Kokonto ya auri masallaci

Bayyana karatun salla a lokacin asirtawa

Zama a raka'a ta farko

Lalurar da ke sa Kabli
Idan an yi ragi a cikin salla, to, za a yi sujadu guda biyu, kafin a yi sallama. Wasu wuraren sujadar ƙabli sun haɗa da:
Mance kabbara biyu ko fiye da haka, amma ban da Kabbarar Harama

Mance faɗin *Sami Allahu liman hamidahu* sau biyu ko fiye da haka

Mance yin tahiya

Yin ragi da ƙari a lokaci ɗaya a salla

Sirranta karatu a wajen bayyanawa

Lalurorin da ba su da Kabli ko Ba'adi

Mance kabbara ɗaya kawai, amma ba ta Kabarar Harama a

Mance faɗin *Sami Allahu liman Hamidahu* sau ɗaya

Mance karatun Alƙunuti

Mance ɗaukaka hannuwa sama a wajen Kabarar Harama

Mance damanta yin sallama

Mance yin tasbihi a cikin ruku'i

Mance yin addu'a a wajen sujada

Mance faɗin *Allahumma Rabbana wa lakal Hamd*.

Jadawalin Yawan Raka'o'i a Sallolin Farilla da na Nafila

A ƙarƙashin wannan jadawali da ke tafe an bayyana yawan raka'o'i da suke a ƙunshe a cikin sallolin farilla da ake yi a kowane yini har sau biyar; sannan kuma aka haɗa da wasu raka'o'in da ake yi na nafila kafin da bayan na farilla. An taƙaita raka'o'in[38] ne a wannan jadawali kamar haka:

Nau'in Salla	Raka'o'in Nafilar Kafin Farilla	Raka'o'in Sallolin Farilla	Raka'o'in Nafilar Bayan Farilla

[38] Waɗannan su ne mafi ƙaranci na nafilolin da za a iya yi a yini ko a sati.

SUBAHIN	2 (Raka'atil Fajri)	2	-
AZAHAR	2 (+ 2 + 2)	4	2 (+ 2 + 2)
LA'ASAR	2 (+ 2 + 2)	4	-
MAGRIBA	2 (- 2)	3	2 (+ 2 + 2)
ISHA'I	2 (+ 2 + 2)	4	2 (+ 2 + 2) 3 (+2 Shafa'i + 1 Witiri)
JUMA'A	2Gaisuwar Masallaci[39]	2	-/ +2(+ 2 + 2)
JUMLA	10 (+12) =22 10(+8)=18(Juma'a)	17 15 Juma'a	9(+12)=21 9(+12)=21Jum
JUMLAR RAKA'O'IN YINI	10 (+12) +17 = 27 (+39) +9 (+12) = 36 (+60) (Babu Juma'a) 10 (+8) +15 = 25 (+33) +9 (+12) = 34 (+54) (Ranar Juma'a)		
JUMLAR RAKA'O'IN SATI ɗAYA	Farillai: 17 ɗ̀6 +15 = 117 (Adadi Kayyadadde) Nafila: 10 + 9 ɗ̀6 +10 + 9 = 133 (Adadi Karami) : (+12 + 12 ɗ̀6 +8 +12 = 164 (Adadi Madaidaici) Jumlar Raka'o'in Farilla da Nafila a sati ɗaya: 414		

Azumi

Azumi shi ne kame baki daga dukkan abin ci ko abin sha ko kowace irin sha'awa daga ɓullowar Alfijir zuwa faɗuwar rana. Azumi kuma ya ƙunshi karatun *Alƙur'ani* da *salati* da *zikiri* da kame kai da sauran ayyuka na ibada da kauce wa ayyuka na alfasha.

Azumi ya ƙunshi waɗannan halaye:

- Babu yin azumi ga kafiri
- Ba a karɓar azumin mahaukaci, sai daga mai hankali.

[39] Ita ce nafila ta kafin sallar Juma'a mafi ƙaranci, amma ana iya yin fiye da haka.

- Wajibi ne mai azumi ya balaga, babu dole ga yara su yi azumi, amma in sun yi ba laifi.
- Dole ne a yi niyyar yin azumi a darensa, ana kwana da jimlatacciyar niyya ne.

Rangwanta Shan Azumi
Shari'a ta rangwanta wa waɗannan mutane da su sha azumi wato su aje azumi saboda wata lalura sai sun fita daga cikinta. Su ne kuwa:

- Mai azumi ya kamu da wata rashin lafiya, kuma yana tsoron ya galabaita, to, ya samu ya sha azumi.
- Mace mai ciki da take tsoron faɗawa cikin lalura.
- Matafiyi da ke dabaibaye da wahalhalu nau'i-nau'i na tare da tafiya.
- Mace mai haila ko jinin biƙi.
- Mutum namiji ko mace mai yawan shekaru, wato tsoho rakwakkwaɓaɓɓe ko tsohuwa rakwakkwaɓaɓɓiya.

Farillan Azumi
Niyya

Kame kai daga abinci ko abin sha ko jima'i ko wata sha'awa

Sunnonin Azumi
Gaggauta buɗa baki

Jinkirta yin sahur

Kame harshe daga munanan maganganu

Abubuwan da ake so ga mai Azumi
- Yin addu'a a lokacin buɗa baki, kamar haka:

Allahumma laka sumtu, wa ala rizƙika afɗartu wa alaika tawakkaltu wa bika amantu, ya wasi'al falali igfirli, walhamdu lillahil lazi a'anani fasumtu, warazaƙani fa afɗartu, fagfirli ma ƙaddamtu wa ma akkartu.

- Yin sahur ko da da ruwa ne kawai a lokacin yin sa

- Kawaici da yin maganganun ƙwarai

- Yawaita ayyukan ibada na kyautatawa

Hajji
Hajji wajibi ne ga Musulmi baligi, mai hankali, mai lafiya, mai hali, mai iya jure wa wahalhalun rayuwa[40], mai ikon ciyar da iyalinsa da duk waɗanda suke a ƙarƙashinsa, tsawon lokacin da zai ɗauka na kwanukan aikin hajji.

Rukunan Hajji
Tsayuwa a Arfa

Ɗawafi

Farillan Hajji
-Ɗaukar harami da hajji daga Miƙati

-Sa'ayi a tsakanin safa da marwa

-Aske gashin kai ko rage shi ko saisaye

[40] Wajabcin hajji ya ɗoru ga namiji da mace bisa waɗannan sharuɗɗa da aka ambata.

-Yanka a ranar suka (Yaumu Nahrin)

-Jifar Aƙabah

-Kwana a Muzdalifa da tsayuwa a Mish'aril Harami.

-Barin ɗayan waɗannan zai sa a yi yanka

Sunnonin Hajji

-Yin wanka kafin a shiga harami

-Tsaftace mayafan aikin hajji

-Yawaita yin talbiyya

-Salla raka'a biyu a yayin shiga harami

-Ziyarar Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama

-Ziyarar Sahabban Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama

-Ziyarar sauran shuhada'u

Zakka

Wajibi ne ga wanda Allah ya ba ikon abin yin zakka ya fitar da ita, kuma ya ba da ita ga waɗanda suka cancanta. Daga cikin sharuɗɗan zakka akwai balaga da hankali da karɓar Musulunci wanda ba shi da waɗannan kuwa ba zai yi zakka ba saboda ba ta rataya a wuyansa ba. Har wa yau ba za a yi wa abu zakka ba sai an mallake shi, mallaka ta haƙiƙa, kuma shi wanda zai fitar da zakka ya zama ɗa ne ba bawa ba.

Nau'o'in Zakka

Zakkar Kono (Fid-da-kai)

Zakkar Zinari da azurfa

Zakkar kayan saye da sayarwa wato ciniki ko kasuwanci

Zakkar Hatsi

Zakkar dabbobi

Zakkar Gidaje da sauran urula

Zakkar sauran abubuwa

Farillan Zakka
Niyya

Cikar Shekara

Kai wa Nisabi

Rashin Cirata

Ladubban Zakka
Ba da ita cikin dadin rai

Killace ta daga idanun mutane

Kasancewarta zaɓin dukiya

Waɗanda ake ba Zakka
Faƙirai[41]

Miskinai

Masu aiki a kan zakka

Waɗanda ake lallashin zukatansu

Fansar wuyaye

Mabarta

[41] Wato matalauta, musamman ƙutu yaumin wato waɗanda ba su da abincin yini.

Aiki a cikin hanyar Allah
Ɗanhanya, ɗantafarki ko matafiyi

3

SASHEN SAURAN AYYUKAN RAYUWA CIKIN IBADA

Sassan da suka gabata an yi magana ne a kan ayyukan ibada bisa shika-shikan Musulunci guda biyar da suka tattaru suka zama ginshiƙan addinin Musulunci. Shi kuma wannan sashi zai zo da bayanai ne a kan matsayin ibada a cikin sauran ayyukan rayuwar ɗan'adam ta yau da kullum. Za a fara da bayyana sakamakon wasu ayyukan mutane a cikin ibada kamar haka:

Sakamakon Wasu Ayyukan Ɗan'adam

An karɓo daga Abu Huraira, Allah ya yarda da shi, sunansa Abdurrahman ɗan Sakhari, cewa shi ya ce, Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce, "Abubuwa uku masu kore azaba ne ga mai yin su, kuma abubuwa uku masu halakar da mai yin su ne, wasu kuma darajoji guda uku zanguna ne da ke ƙara ɗaukaka mai yin su a ranar Tashin Kiyama, sannan wasu ukun kuma kaffara ne da ke shafe zunuban mai aikata su:

Uku masu Kore Azaba su ne:
-Tsoron Allah, maɗaukaki, a zuci da zahiri wato a bayyane ko a ɓoye.

-Kyautace niyya a halin talauci ko wadata.

-Yin adalci a lokacin yarda ko hushi.

Uku masu Halakarwa su ne:

-Tsananin sakaci da zai kai ga sa wa a kasa kiyaye haƙƙoƙin Allah da na abokan halitta.

-Ɗaukar kai da ɗagawa.

-Bin soye-soyen zuciya.

Uku na Darajojin Ɗaukaka su ne:
-Yawaita yin sallama a tsakanin mutane daɗa da wanda aka sani ne ko wanda ba a sani ba.

-Ciyar da baƙi abinci da mai jin yunwa ko mabuƙaci.

-Sallolin dare alhalin mutane suna ta sharɓar barci.

Uku na Kaffara kuma su ne:
-Yawaita Alwala.

-Cire takalma a wurin jama'a.

-Jiran salla bayan salla don a sallace ta a Masallaci.

Maganin Cutar Zunubai

An karɓo daga Anas ɗan Maliku, Allah ya yarda da shi, ya ce: Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce: "Shin ba zan shiryar da ku a kan cutar zunubanku da maganinta ba"? suka ce "I, muna so ya Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama". Annabin Rahama ya ce: "Haƙiƙa cutar zunabanku, maganinta yawaita yin tuba da neman gafarar Allah wato Istigfari" Dailami ya ruwaito wannan Hadisi.

An karɓo kuma daga Ibn Abbas, Allah ya yarda da shi, cewa shi ya ce: Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce, "Wanda ya maƙale wa yin Istigfari (yana mai tuba ga Ubangijinsa, ya lazimci yin haka) Allah zai sanya masa mafita daga kowane irin ƙunci, zai yaye masa kowane irin baƙin ciki,

ya kuma azurta shi daga ta gefen da ba ya zato" (Abu Dawuda da Ibn Majah suka ruwaito shi).

Kaɗan daga cikin kalmomin Istigfari su ne:

"Astagfirul lahal azim", wato ina mai tuba zuwa ga Allah, mai girma, ina kuma mai neman gafararsa. Ko kuwa, *Astagfirul lahal azimil lazi la'ilaha illa huwa hayyal ƙayyum.*

Akwai kuma:

Tsarki ya tabbata ga Allah, Godiya ta tabbata ga Allah, babu abin bauta da gaskiya, sai Allah. Allah, mai girma, ina neman gafararka ya Allah. Babu dabara babu ƙarfi, sai daga wurinka ya Allah, mai girma mai ɗaukaka.

Wasiyyar Ubangiji ga Manzonsa, sallallahu Alaihi wa Sallama, don Sauran Mutane su Kwaikwaya:
Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce:

"Ubangijina ya yi mini wasiyya da abubuwa guda tara:

-Ya yi mini wasiyya da tsoron Allah a bayyane ko a ɓoye.

-Yin adalci a halin yarda ko hushi.

-Kyautace niyya a halin talauci ko wadata.

-Yafe wa wanda ya zalunce ni.

-In ba wanda ya hana mini.

-In sadar da zumunta ga wanda ya yanke a gare ni.

-In zama mai tuntuntuni a ko da yaushe.

-Tausayi ya zama ambatona.

-Tunanina ya zama farin ciki.

Riƙo da Halaye Guda Biyu

Tirmizi ya ruwaito daga Ibn Umar cewa, lalle Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce: "Halaye guda biyu wanda ya kasance tare da su, Allah zai rubuta shi mai godiya mai haƙuri wato zai zama mutum mai godiyar Allah. Wanda bai same su ba kuwa, Allah ba zai rubuta shi a cikin masu godiyarsa da haƙuri ba.

Ko saurara! Wanda ya yi dubi a addininsa zuwa ga wanda yake sama da shi (ga yin bauta) ya yi koyi da shi, sannan ya yi dubi a duniyarsa bisa ga wanda yake koma bayansa, sai ya gode wa Allah kan baiwar da ya yi masa, shi ne wanda za a rubuta mai godiya mai haƙuri.

Kuma wanda ya yi duba a addininsa zuwa ga koma bayansa, haka kuma ya yi dubi a duniyarsa, zuwa ga wanda yake sama da shi, ya yi kaico a kan abin da ba shi da shi, ko ya kuɓuce masa, Allah ba zai rubuta shi mai godiya mai haƙuri ba.

Kwaɗaitarwa kan Aikata Alheri

Wata rana Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya kasance yana zaune tare da Sahabbansa. Allah ya yarda da su, sai ga Mala'ika Jibrilu, aminci ya tabbata a gare shi, ya zo masa. Mala'ika Jibrilu ya ce da Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama: "Allah, mai girma da ɗaukaka ya aiko ni ne. ya ji zancenku, ya kuma hore ka, ya Manzon Allah, da ka yi mini tambaya a kan abin da nake so, da a ce ina ɗaya daga cikin mutanen duniya.

Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce, Me kake so Jibrilu in da a ce ka kasance a cikin mutanen duniya? Mala'ika Jibrilu ya ce:

- Shiryar da mutanen kirki zuwa ga tafarki madaidaici;
- Da taimakon baƙi da suka yi nufi da aikinsu domin Allah mai girma;
- Da taimakon masu iyali da ke cikin tsananin rashi.

Sannan Mala'ika Jibrilu, aminci ya tabbata a gare shi, ya ƙara cewa, Ubangiji mai girma da ɗaukaka yana son abubuwa guda uku daga wajen bayinsa. Su ne kuwa:

- Baza himma a cikin bautar Allah;
- Da kuka a halin yin nadama, bisa ga wani aiki na saɓo da aka yi;
- Da yin haƙuri a halin rashi, bisa samuwar wata buƙata.

Baza Himma a Cikin Ibada

An karɓo daga Kabilu ɗan Hazim, Allah ya yarda da shi, cewa shi ya ce: "Na ji Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana cewa: "Ya ku mutane ku biɗi Aljanna da ƙoƙarinku, ku nisanci wuta kuna masu guje mata da ƙoƙarinku. Ku sani lalle mai neman Aljanna ba ya barci, lalle mai guje wa wuta ba ya barci. Aljanna na zagaye da abubuwan ƙi, ita ko wuta tana dabaibaye da abubwan jin daɗi da sha'awace – sha'awace, to, kada su halakar da ku daga samun daɗaɗan Lahira".

Musibu uku na Karshen Duniya

Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya ce: "Wani lokaci zai zo ga al'ummata da za su dinga gudun malamai da masu hukunce-hukuncen ibada (Fiƙhu) wato suna masu ƙin son zama da su. To, Allah zai jarabce su da jarabtu ko fitinu guda uku:

-Allah zai ɗauke albarka daga abubuwan tsiwurwurtarsu ko bukatun rayuwarsu.

-Allah zai ɗora musu shugabanni azzalumai.

-Za su bar duniya ba tare da imani ba wato su mutu babu imani". Allah ya kiyaye mu, amin.

Sakamakon Wulaƙanta Abubuwa Guda Biyar

An ruwaito daga Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya ce "Duk wanda ya wulaƙanta abubuwa guda biyar, haƙiƙa ya halaka. Su ne kuwa:

- Wanda ya rena malamai har ya kasance ba ya mutunta su, ya yi hasara a addininsa domin malamai ne taskar ajiyar shari'a kuma masu koyar da ita.
- Wanda ya wulaƙanta sarakuna ya yi hasara a duniyarsa domin su ne ke jagorancin al'amuran duniya, sannan linzaminta yana hannuwansu.
- Wanda ya yi watsi da mutanen da yake maƙwabtaka da su a mazauni ko a wurin ma'amala, hulɗar yau da gobe, ya yi hasarar samun amfani da alherin da ke cikin taimakon juna. Manzon Allah ya ci gaba da cewa, "Na rantse da wanda raina yake hannunsa, imanin bawa ba ya cika, sai ya so ga maƙwabcinsa abin da yake so ga kansa". An kuma ruwaito

Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce: "Haƙiƙa Allah, mai girma da ɗaukaka, yana son mutumen da yake da mugun maƙwabci wanda yake cutar da shi, amma ya yi haƙuri a kan cutar da shi da yake yi, ya yi ta tsiwurwurtar haƙuri da shi har rayuwa ta yi masa ƙunci ko Allah ya karɓi ransa" (Buhari ne ya ruwaito wannan Hadisi).

- Wanda ya wulaƙanta 'yan'uwansa na tsatso ya yi hasarar jin daɗin zaman 'yan'uwantaka da soyayyarsu.
- Wanda ya wulaƙanta iyalinsa wato matarsa ko matansa, ya yi hasarar samun jin daɗin rayuwa da take wanzuwa a tsakanin zaman iyali.

Mutanen Kwarai da Ashararai

An karɓo daga Abu Hurairata, Allah, ya yarda da shi, ya ce, Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce, "Zaɓaɓɓun al'umma su ne waɗanda suka shaida babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah, kuma Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, Manzon Allah ne. Idan suka munana su nemi gafara, idan suka yi tafiya su yi ƙasaru a sallolinsu, su kuma ajiye azuminsu.

Lalle ashararun al'umma su ne waɗanda aka haife su, suka girma a cikin ni'ima, amma babbar himmarsu abinci nau'i-nau'i da nau'o'in abin sha. Idan suka yi magana su kambama, idan suka yi tafiya su yi taƙama. Kaico ga waɗanda suke masu kauce wa hanya, ƙasƙantattu, masu ci na ɓarna, masu barin biyayyar Allah da rashin istiƙama, ko tsayuwa ta sosai a cikin bautar Allah".

Mace mai Haila

An ruwaito daga A'isha, Allah ya yarda da ita, cewa ita ta ce, Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabata a gare shi, ya ce: "Babu wata mace da take haila, sai hailar nan tata ta zama kaffara wato wanki daga zunubanta da suka shuɗe. In kuma ta ce a farkon jininta na haila:

> *Godiya ta tabbata ga Allah a kowane hali. ina neman gafarar Allah daga kowane irin zunubi.*

Allah ya yi mata shamaki ga wuta, kuma an sauwaƙe mata siratsi, an lamunce mata daga azaba, an ba ta darajar shahidai arba'in, musamman idan ta zamanto mai ambaton Allah cikin hailarta" wato tana mai maimaita cewa:

> *Tsarki ya tabbata ga Allah, Godiya ta tabbata ga Allah, babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah, Allah mai girma, babu dabara babu ƙarfi, babu tsimi babu tanadi sai daga wajen Allah.*[42]

Bin Umurnin Miji ga Mace

An hakaito wani mutum a zamanin Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya fita yaƙi. Ya ce da matarsa "Kada ki fita daga wannan gida sai na dawo miki", sai mahaifinta ya kamu da rashin lafiya. Ta aika ɗan saƙo wajen Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, tana neman izinin fita. Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce da ita, "Ki bi umurnin mijinki". Ta yi ta yi wa Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, aike, manzo bayan manzo, shi ko sai ya dinga ce mata, "Ki bi umurnin mijinki". Sai ta bi dokar

[42] Wato 'Subhana lillahi walhamdu lillahi wa lama'abudi bilhaƙƙi illalla walahaula walaƙuwata illa billahil aliyil azim'.

mijin nata, ba ta fita ba. Mahaifinta har ya rasu, ba ta gan shi ba, ta yi haƙuri a kan haka har zuwa ranar da mijinta ya dawo gare ta. sai Allah ya yi wahayi ga Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, cewa Allah ya gafarta mata bisa biyayyar da ta yi wa mijinta.

Sakamakon Rashin bin Umurnin Miji ga Mace

An ruwaito daga Abu Zarri, Allah ya yarda da shi, cewa shi ya ce: "Na ji Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana cewa "Kowace irin mace ce, ta ce ga mijiinta, "Allah ya la'ance ka wato dai ta zage shi tana mai zaluntarsa, to, Allah ya la'ance ta da dukkan sauran halittunsa, sun la'ance ta".

Sakamakon Matar da Take Kallafa wa Mijinta Abin da ba ya Iyawa

An ruwaito daga Abdurrahman ɗan Auf, Allah ya yarda da shi, cewa shi ya ce, "Na ji Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, yana cewa: "Kowace irin mace ta sa wa mijinta baki a sha'anin ciyarwa ko ta ɗora masa abin da ba ya iyawa, Allah ba zai karɓi ɗugo daga aikinta ba, kuma ba za ta sami rahamarsa ba".

Sakamakon Fitar Mata ba da Sanin Mijinta ba ko Miji ya Bari ta Sanya Turare ta Fita

An ruwaito daga Ɗan'abbas, Allah ya yarda da shi, cewa shi ya ce, "Na ji Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana cewa, "Kowace irin mace ta fita daga gidan mijinta ba tare da izininsa ba, duka abin da rana da wata ke hudowa a kansa zai la'ance ta, har sai ta dawo daga wannan fita da ta yi".

An daɗa ruwaitowa daga Ɗan'abbas cewa shi ya ji Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, yana faɗin, "Kowace irin mace ta fita daga ƙofar gidanta, ta yi ƙawa, ta ƙansasu da ƙanshin turare, mijinta kuma ya yarda da haka, Allah zai gina wa mijin gida a cikin wuta a kan kowane taki da ta yi. Allah ya kiyaye mu, amin.

Mata mai Kyautata wa Mijinta

An ruwaito daga Abdullahi Ɗanmas'udu, Allah ya yarda da shi, cewa ya ce, "Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya ce "Idan mace ta wanke tufafin mijinta, Allah zai rubuta mata lada dubu, ya shafe mata zunubai dubu biyu, sannan duk abin da rana da wata ke hudo haskensu a gare shi zai dinga nema mata gafara. Darajarta kuma za ta ɗaukaka sau dubu" (Abu Mansur ne ya ruwaito shi daga Musnadil Firdausi).

Wasu Mata da Sakamakon Ayyukansu

An ruwaito daga Sayyadi Aliyu Ɗan'abiɗalib, Allah ya yarda da shi, cewa shi ya ce, "Na shiga da ni da Faɗima wurin Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sai muka same shi yana kuka. Muka ce "Mene ne ya sanya ka kuka ya Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama,? Sai ya ce, "Na ga mata a daren da aka yi tafiya da ni zuwa sama cikin tsananin azaba, shi ne na tuna halin da na baro su a ciki, sai nake kuka!

Faɗima ta tambayi Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, cewa "Me ya gani? Manzon Allah ya ce, "Na ga wata mace an sargafe ta da gashin kanta, kuma kwanyar kanta na darara.

Na ga wata mace an rataye ta da harshenta, sannan an ɓullo da hannunta ta bayanta daga ƙirjinta, ana zuba mata ruwan zafi a cikin wuyanta.

Na ga wata mace an rataye ta da mamanta ta bayanta, ana zuba mata ruwan zaƙumi a wuyanta.

Na ga wata mace wadda aka sargafe, an ƙuƙunta ƙafafunta da hannuwanta zuwa ƙeyarta. Sannan an zuba mata kunamu da macizai suna cizonta, suna kuma saranta.

Na ga wata mace tana ci daga naman jikinta, wuta tana ci daga ƙarƙashinta.

Na ga wata mata ana gutsurar jikinta da almakashi na wuta.

Na ga wata mace kanta ya koma tamkar kan alade, jikinta kuma kamar jikin jaki, ana yi mata nau'o'in azaba dubun dubata.

Na ga wata mace a kan siffar kare, kunamu da macizai na shiga gaba gare ta, suna fita ta ɗuwawunta, Mala'iku na dukan kanta da kulake da kokarar wuta.

Daga nan Faɗima ta tashi, ta ce "Ya Babana, ba ni labarin ayyukan da waɗannan mata suke aikatawa". Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce: "Ya Faɗima":

- Ita dai wadda aka rataye da gashinta, ta kansance ba ta rufe gashin kanta daga idon maza.
- Wadda aka rataye da harshenta tana cutar da mijinta da harshenta. Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ci gaba da cewa duk matar da take cutar da mijinta da harshenta, wato ba ta sirranta abubuwa tsakaninsu a ranar Tashin Kiyama, Allah zai mayar da tsawon harshenta kamu saba'in, a nannaɗe mata shi a wuyanta. Kuma Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya ce, "Babu wata mace da za ta ce ga mijinta ban ga wani alheri daga gare ka ba, ba

ka tsinana mini komai ba, sai Allah ya shafe aikin alherinta kwatankwacin shekaru saba'in ko da ta kasance tana azumtar kowace rana, kuma tana rayar da kowane dare.

- Wadda aka rataye da mamanta ta kasance tana renon 'ya'yan wasu ba tare da umurni ko izinin mijinta ba.
- Wadda aka sargafe da ƙafafuwanta kuma ta zamanto tana fita daga gidan mijinta ba tare da izininsa ba, kuma ba ta wankan haila ko na jinin biƙi.
- Amma wadda take ci daga naman jikinta ta kasance tana yin ƙawa don maza su gan ta, kuma tana mai yin rangwaɗa.
- Amma wadda ake yankan jikinta da almakashin wuta ta kasance tana jan ra'ayin mutane da kanta. Wato tana jan hankalinsu da ƙawarta, kuma tana son wanda duk ya gan ta ya so ta.
- Ita ko wadda aka ƙuƙunce ta zamanto tana iya yin salla da azumi, amma ba ta yi wato ba ta yin alwala, ba ta salla, ba ta wankan janaba.
- Amma wadda kanta ya zama kamar kan alade da jikin jaki ta kasance magulmaciya, kuma maƙaryaciya.
- Wadda ke a kan surar kare ta kasance tana ƙin mijinta tare da rataya masa abin da ba ya iyawa na hidimar gida.

Kafa Hujja da Mutane Huɗu

Allah mai girma da ɗaukaka zai kafa wa mutane hujja da wasu bayinsa guda huɗu, kamar yadda wannan hadisi ya bayyana:

An karɓo daga Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, cewa shi ya ce: Lalle Allah mai girma da

ɗaukaka a ranar Tashin Ƙiyama zai kafa hujja da mutane huɗu a kan rukunonin jama'a huɗu. Su ne kuwa:

-Allah zai kafa wa mawadata (Masu kuɗi) hujja da Annabi Sulaiman ɗan Dawuda, amincin Allah ya tabbata a gare su, inda Allah zai ce da su, don me kuka bar ibada? Idan suka ce, mu mun shagalta da dukiya ne da harkokin gudanarwa. Allah zai ce musu, wace irin masarautar mulki ce ta fi ta Annabi Sulaiman, kuma wace irin dukiya ce, ta fi tasa, amma shi bai bar yi wa Allah ibada ba.

-Allah zai kafa wa bayinsa hujja da Annabi Yusuf, inda za a ce da su, don me kuka bar ibadar Allah? Idan suka ce, mu mun shagalta da hidimomin iyayen gijinmu ne. Allah zai ce musu bawana Yusuf ya zauna a ƙarƙashin Sarkin Misra da Matarsa, amma shi bai bar bautar Allah ba.

-Allah zai kafa wa marasa lafiya hujja da Annabi Ayyuba inda za ya ce da su, don me kuka bar bautar Allah? Idan suka ce, mu marasa lafiya ne. Allah zai ce da su, bawana Ayyuba ya yi rashin lafiya mai tsanani, amma bai bar bautar Allah ba.

-Allah zai kafa wa matalauta hujja da Annabi Isa, inda za ya ce da su, don me kuka bar bautar Allah? Idan suka ce, mu mun shagalta da tsanance-tsanancen talauci ne. Allah zai ce da su, "Bawana Isa, ya fi duk wanda ke a bayan ƙasa talauci, bai mallaki komai a duniya ba, ba shi da gida, ba shi da dukiya, ba shi da mata, ba shi da komai, amma shi bai bar bautar Allah ba.

Ku yi dubi ya ku 'yan'uwa yadda Allah ya kafa hujja a kan waɗannan mutane da waɗannan bayinsa da suka kyautace niyya da aiki a wajen yi masa bauta. Allah ya tabbatar da zukatanmu a kan imani da yi masa bauta, amin.

Alamomin Tashin Kiyama

Shehu Usmanu Ɗanfodiyo, Allah ya yarda da shi, ya yi wa Musulmi nasiha, ya faɗakar da su game da alamomin kusantowar Tashin Kiyama. Ya bayyana cewa, Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya tambayi Mala'ika Jibrilu, "Yaushe ne sa'a za ta tsayu?" Jibrilu ya ce "Ba wani mai rai ɗaya da ya san lokacin da za a yi Tashin Kiyama, sai Allah, mai girma da ɗaukaka. Allahu yana cewa a cikin *Alƙur'ani*, "Gare shi ne za a mayar da sanin sa'a, babu wani wanda ya san lokacinta, sai shi Allah". Amma akwai alamomin gane kusantowar lokacinta, Ɗan'abbas, Allah ya yarda da shi, ya ce, "Sa'a ba za ta tashi ba, sai a kan ashararun mutane". Ka'abul-Ahbari ya faɗi alamomi arba'in (40) na kusantowar tsayuwar Alƙiyama. Wasu daga cikinsu su ne:

-Barbazuwar ayyukan ɓarna tsakanin sarakuna da malamansu da talakawansu.

-Mahukunta tamkar alƙalai su dinga ɓoye gaskiya saboda duniya da dauɗar duniya.

-Malamai za su bar matsayinsu, su taushe littattafan faɗar gaskiyarsu, su ɗaukaka duniya fiye da komi a gabansu.

-Yawaita ƙeta tsakanin zukatan maza da mata.

-Mawadata ba su jinƙan faƙirai da miskinai wato dai mawadata ba su taimakon marasa ƙarfi.

-Manoma su daina fitar da zakka.

-Garuruwa su zama kusa da juna maimakon nisantarsu.

-Ba za a sami aboki ba sai mayaudari.

-Matan aure su zama tamkar abokan juna, ba ma'aurata ba.

-Taƙaita tsawon yini da dare wato lokaci zai tauyu.

-Jahilai za su dinga jayayyar isgili da malamai.

-Yi wa addini riƙon sakainar kashi.

-Malamai za su dulmuya cikin sa kyawawan manyan tufafi kuma ba za su dami kansu da sauraron karatun *Alƙur'ani* ba.

-Malamai ba su damu da kyautatuwar yanka ba.

-Za a yawaita yaƙe-yaƙe a duniya.

-Mutane za su shagala da yawan gine-gine.

-Za a fifita zina a kan aure.

-Yawaitar ƙananan yara wato yawan haihuwa.

-Fifita ƙarya a kan gaskiya da yawaita ƙage da jamhuru ga abokan zama.

-Yawaitar 'ya'ya mata a kan 'ya'ya maza wato mata su fi maza yawa.

-Ɗa ba ya jin tsoron iyayensa wato ba ya ganin girmansu.

-Ɗa ba zai gaji mahaifinsa ba.

-Yawaitar cututtuka a jikunkunan mutane.

-Bayyanar Dujjal.

-Ɗullowar rana daga yamma ta faɗi gabas.

-Bayyanar Yajuju da Majuju.

-Ɗaukewar ainihin ran rayuwa kamar haka:

-Albarkar ƙasa;

-Tausayi daga zukata;

-Adalci daga shugabanni;

-Kunya daga mata;

-Haƙuri da wadatar zucci daga matalauta;

-Tsantseni da gudun duniya daga malamai;

-Jinƙai daga mawadata;

-*Alƙur'ani* daga Makaranta;

-Imani daga Rayuwa.

4

SHASHEN SIRAR ANNABAWA DA MANZANNI

Haƙiƙa ilimin tarihi gaskiya ne. kuma yin waiwaye a cikin gurabun mazaje masu girman daraja da matsayi da manya-manyan malamai abu ne da yake ƙara wa mutum basira a addininsa da duniyarsa, mai kuma neman sanin haka kuwa mai ƙoƙarin hangen nesa ne. Allah ya zaɓi wasu mutane mazaje ya turo su zuwa ga sauran bayinsa don su shiyar da su zuwa ga abin da yake alheri a gare su a duniyarsu da lahirarsu. An riga an yi bayani a sashen aƙida, Annabawa bayi ne na Allah tsararru, masu gaskiya da amana da kaifin nutsuwa da fahimta da isar da annabci. An keɓe wannan sashe ne inda za a kawo bayanai game da yadda Annabawa da Manzanni suka gudanar da rayuwarsu, a ga irin gwagwarmayar da suka sha yi a tsakanin al'ummominsu daban- daban.

Sira, wani fage ne na ilmi da yake koyar da sanin rayuwar zaɓaɓɓun mutane daga wajen Allah da suka haɗa da Annabawa da Manzanni da Sahabbai da waliyyai da malamai da sauran masu jihadi don kyautata kalmar Allah. Har wa yau kuma sira wata hanya ce wadda ake sanin tarihin rayuwar fajiran mutane, musamman waɗanda suka juya wa addinin Musulunci baya kamar Abu Jahil da Bil'amu ɗan Ba'ura da sauransu.

A wannan sashe za a kawo wasu bayanai a kan halittar mutum ɗan'adam da dalilan da suka sa aka halicce shi, sannan da bayanin Annabawa da Manzanni da matsayinsu a tsakanin sauran bayin Allah 'yan'adam da zaɓinsu da aka yi aka aiko su Annabawa ko Manzanni. Daga nan kuma za a zo da tarihin

Annabin Rahama, sallallahu alaihi wa sallama, daga haihuwarsa zawa wafati nasa.

Halittar Mutane da Annabawa da Manzanni

Allah, mai girma da ɗaukaka, ya halicci mutane, maza da mata bisa aƙidar Musulunci, daga tsatson Annabi Adamu, alaihis salam, wanda yake farkon halitta da Ubangiji ya halicce shi daga turɓaya. Allah yana cewa, "Lalle ne misalin Isa a wurin Allah kamar misalin Adamu ne. (Allah) ya halitta shi daga turɓaya, sannan kuma ya ce masa: "Ka kasance, "sai yana kasancewa" (Ali Imrana, aya ta 59). Akwai kuma inda Allah yake cewa, "Kuma a lokacin da Ubangijinka ya ce wa Mala'iku, "Lalle ni mai halittar wani jiki ne daga ƙeƙasasshen yumɓu wanda ya canja. To, idan na daidaita shi, kuma na hura daga ruhina a cikinsa, to, ku faɗi a gare shi, kuna masu yin sujada" (Hijri, aya ta 28 – 29). Daga nan, sai Ubangiji ya halicci Hauwa'u wadda ta zama matarsa.

Ashe ke nan halittar mutum ta zamanto ne daga laka da turɓaya kamar yadda Allah ya faɗa a cikin wannan aya, "Shi ne (Allahu) wanda ya halitta daga laka, sa'an nan kuma ya yanka ajali, alhali wani ajalin ambatacce yana wurinsa, sa'an nan kuma kuna yin shakka" (An'am, aya ta 2). Domin haka, mutum halitta ce ta Ubangiji wadda ya sanya mata rai da hankali don ta yi masa bauta. Allah ya sanya zuriyya da ta fito daga tsatson Adamu da Hauwa'u suka zama ƙabilu da jinsuna daban-daban a farfajiyar sassan duniya. Domin haka, Allah yana cewa. "Ya ku mutane lalle ne mu, mun halitta ku daga namiji da mace, kuma muka sanya ku dangogi da ƙabilu domin ku san juna" (Hujurat, aya ta 13).

Mutanen duniya kaf daga mafari ɗaya suka fito, daga baya ne suka rarrabu da juna saboda bambanci a wajen riƙo da umurnin Allah ko haninsa. Allah yana cewa, "Kuma

mutane ba su kasance ba, face al'umma guda, sa'an nan kuma suka saɓa wa juna, kuma ba domin wata kalma wadda ta gabata daga Ubangijinka ba, da an yi hukunci a tsakaninsu a kan abin da yake a cikinsa suke saɓa wa juna" (Yunusa, aya ta 19).

Bayan Allah ya gama halittar mutum ya daidata shi, ya yi masa abubuwan da zai bukata a zagaye da shi, sai ya neme shi da ya yi masa bauta. Sa mutum ya yi ibada ga Allah baiwa ce a gare shi, kuma mahaliccinsa yana son sa, yana ƙaunarsa, domin wanda ba a ƙauna shi ake bari haka nan sagaga, ba wata shiryarwa, ballantana a name shi da ya yi wani abu. Ubangiji Jalla Jalalahu, ma yana cewa:

> "*Shin mutum na zato na bar shi haka nan sagaga (wato babu nufin kome game da shi?). Ashe bai kasance ɗugo na maniyyi ba, wanda ake jefarwa (a cikin mahaifa), sa'an nan ya zama gudan jini, sa'an nan Allah ya halitta shi, sa'an nan ya daidaita gaɓoɓinsa, sa'an nan ya sanya daga gare shi nau'o'i biyu, namiji ko mace? (Kiyama, aya ta 36 – 39).*

Tun da shi kansa mutum ba zai so a bar shi haka nan sudam ba, sai aka neme shi da ya yi wa Allah bauta. Shi ne Allah yake cewa, "Kuma ban halitta aljannu da mutane ba, sai don su bauta mini. Ba ni nufin (samun) wani arziki daga gare su, ba ni nufin su (yi hidimar) ciyar da ni. Lalle ne Allah shi ne mai arzurtawa, mai ikon yi, mai cikakken ƙarfi" (Dhariyat, aya ta 56 – 58). Daga nan, sai Allah ya yi kiran mutane zuwa ga yin ɗa'a bisa wannan bauta da ya halicce su kawai domin ita inda ya ce:

"Ya ku mutane! Ku bi Ubangijinku da taƙawa, wanda ya halitta ku daga rai guda, kuma ya halitta, daga gare shi, ma'auransa, kuma ya watsa daga gare su maza masu yawa da mata. Kuma ku bi Allah da taƙawa wanda kuke roƙon juna da (sunan) shi, da kuma zumunta, lalle ne Allah ya kasance, a kanku, mai tsaro ne" (Nisa'i, aya ta 1).

Domin Allah ya taimaka wa mutane amsa kiran sa ga yi masa bauta cikin sauƙi, sai ya zaɓi wasu mutane daga cikinsu suka zama Manzanni na isar da saƙon yadda za a yi masa bauta. Ya fadi yadda yake son a bauta masa ta hannun waɗannan zaɓaɓɓu mutane, Manzannin Allah. Su kuma waɗannan Manzanni ya haɗa su da Mala'ikunsa a matsayin jekadunsa, inda su Manzannin za su dinga karɓar hukunce-hukunce ibada ta hanyar Mala'ika daga wajen Allah. Allah yana cewa:

"Mutane sun kasance al'umma guda. Sai Allah ya aiki Annabawa suna masu bayar da bishara kuma masu gargadi, kuma ya saukar da littafi da gaskiya tare da su domin (Littafin) ya yi hukunci a tsakanin mutane, a cikin abin da suka saɓa wa juna a cikinsa" (Baƙara, aya ta 213).

Dukkan jinsunan da suka yi imani da Allah tun daga Annabi Adamu har zuwa ga Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, sun zama al'umma ɗaya. Babu wani saɓani a tsakaninsu. Al'ummar Musulmi duka al'umma ɗaya ce, ko da yake Annabawa sun zo daban-daban a kuma cikin lokuta masu nisa tsakaninsu, da harsuna mabambanta, saboda

dukansu aƙida ɗaya ce gare su, ta imani da cewa Ubangiji guda ɗaya ne, kuma Manzanninsa bayinsa ne zaɓaɓɓu. Su kuma waɗanda suka fita daga cikin wannan aƙidar su ne suka rarrabu ƙungiya–ƙungiya. Ga Musulmi, Allah ne abin yi wa bauta: "Lalle ne wannan ita al'ummarku, ta zama al'umma guda, kuma ni ne Ubangijinku, sai ku bauta mini". A wajen ɗa'a ba a tsaya ga yi wa Allah kawai ba, a'a, har da Manzanninsa, "Ka ce; "Ku yi ɗa'a ga Allah da Manzo. To, amma idan sun juya baya, to lalle ne Allah ba ya son kafirai" (Ali Imrana, aya ta 32).

Allah, subhanahu wa ta'ala, ya aiko Manzanni don su zama wakilansa a bayan ƙasa, da za su isar da umurce-umurcensa da hane-hanensa waɗanda suka tattaru suka haɗa shari'ar Allah. Manzannin da Allah ya aiko su da manzanci, tsararrru ne waɗanda Allah yake kiyaye su daga faɗawa cikin miyagun ayyuka da ke ɓata al'umma. Su masu shiryarwa ne ba masu ɓatawa ba. Allah ya isar da shari'ar Musulunci ta hanyarsu zuwa ga sauran bayinsa, 'yan'adam. *Annabi* shi ne wanda aka ba wani umurni, amma ba a hore shi da ya sanar da shi ga kowa ba, sai dai don ya amfanu da shi. *Manzo* kuwa shi ne wanda aka aiko shi da shari'a, sannan aka umurce shi da ya isar da ita zuwa ga al'ummarsa. Allah ya zaɓi Annabawa daga cikin mutane har guda dubu ɗari da dubu ashirin da dubu huɗu (124,000), sannan ya sake tace wasu daga cikinsu suka zama Manzanni, adadinsu su kuma, su ɗari uku ne da goma sha uku (313) a kan ittifaƙin yawan malamai. *Alƙur'ani* da sunnar Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, sun zo da sunayen wasu Annabawa kamar haka:

Adamu
Halliru
Nuhu

Idrisu
Ibrahim
Ishaka
Ya'aƙubu
Yusufu
Yahya
Yunusa
Dawuda
Iliyasa'u
Zakariya'u
Salihu
Shisu
Zulƙifli
Luɗu
Armiya'u
Ash'iya'u
Askandar
Sulaiman
Musa
Shu'aibu
Haruna
Ayyuba
Hudu
Daniyal
Lukman
Uzairu
Isa
Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama[43]

[43] Abin lura a nan shi ne ba an jera sunayen waɗannan Annabawa da Manzanni ne gwagwadon bin layin zamani da lokaci da shekarunsu

Dukkan Manzannin da Allah ya aiko ba su da wani bambanci na shari'a, suna kira ne a kan abu ɗaya wato kaɗaita Allah da yin hani ga yi wa Allah shirka. Kowane Manzo kuma ana aiko shi ne ga al'ummarsa, illa Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, wanda ya zama Manzon ƙarshe, kuma an aiko shi ne zuwa ga dukkan duniya gaba ɗaya, sannan ya iyar da cikasa kyawawan halaye da Annabawa da Manzanni waɗanda suka rigaye suka fara zowa da su. Musulunci a lokacin Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, yana da sauƙi wajen gudanarwa da wajen tsayar da hukunci. Allah ya kuma haɗa dukkan shari'ar da aka saukar wa sauran Annabawa a cikin *Alƙur'ani*. Haka nan kuma an ba Annabi Muhammadu wasu sababbin hukunce-hukuncen shari'a ƙari ga waɗanda suka gabace shi.

Sirar Annabi Muhammadu,
Tsira da Amincin Allah su Tabbata a Gare shi

Bibiyar tarihin rayuwar Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, bisa kyautace niyya, yana daga cikin neman lada da samun ilmi mai yawan amfani. Sannan mutum zai sami babbar riba idan ya yi kwaikwayo da nagartattun ayyukansa, sallallahu alaihi wa sallama. Wajibi ne wajabci kuma a kan ɗaɗaikun Musulmi su yi riƙo da gurabun rayuwar Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, kuma su yi aiki da su bisa kyautace niyya. Za a kwaikwayi halayensa da ayyukansa da riƙo da shari'ar da ya zo da ita daga wurin Allah.

---

mabanbanta ba. An dai kawo sunayensu ne a ta la'akari da jeranta su wani bayan wani.

Da ma an ce kyawon ilmi aiki da shi. A wannan sashe an tsakuro bayanai ne a ƙan ƙyas na daga cikin rayuwar Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, aka zo da su, kamar haka:

Haihuwar Manzon Allah,
Sallallahu Alaihi wa Sallama

An haifi Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su kasance a gare shi, a garin Makka, ranar Litinin, sha biyu (12) ga watan Rabi'ul Auwal, shekara da ake ambata, shekarar giwa, daidai da 20 ga watan Afrilu, shekarar 571 Miladiyya. Ana kiran ta shekarar giwa, saboda Abrahata, Sarkin Habasha da ya aiko rundunar mayaƙa, suna haye bisa manya-manyan giwaye, wai don su rushe Ɗakin Ka'aba. Sai Allah ya halakar da su, ya ruguza makircinsu don kiyaye wa ga ɗakinsa mai alfarma. Daga nan ne Larabawa suka dinga jingina tarihin aukuwar abubuwa a wannan shekara da shi.

Gari da Ƙabilar Manzon Allah,
Tsira da Amincin Allah su Tabbata a Gare shi

Garin Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, na farko shi ne Makka inda Ɗakin Allah na Ka'aba yake. Ƙabilarsa kuma ita ce Ƙuraishi wadda ta shahara da hikima da jaruntaka da karimci da ɗaukar gabata. Saboda haka ne ƙabilar Ƙuraishawa ta fi dukkan sauran ƙabilun Larabawa ɗaukaka da shahara. Ƙuraishawa sun shagaltu da kasuwanci da taimakon mabuƙata da girmama baƙi masu zuwa ziyarar Ɗakin Allah, tana kuma da matsayi babba a tsakanin ƙabilun Larabawa.

Ƙusayyu ɗan Kilabu shi ne ya fara haɗa kan ƙabilar Ƙuraishawa waje ɗaya, har sauran ƙabilun Larabawan Makka suka sakar musu jan ragamar shugabanci. Ƙusayyu na daga cikin shugabannin da aka zaɓa aka naɗa, masu jagorancin

kula da ɗakin Allah na Ka'aba. Ya zama shi ne mai zartar da hukunci kan al'amura. Bayansa kuma, sai aka zaɓi Hashimu ɗan Abdil-Manafi, daga shi kuma sai Abdul-Muɗɗalib ɗan Hashim; waɗannan kuma duk suna cikin kakannin Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama.

Madina, mai haske da hasken Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ita ce ta zama gari na biyu ga Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama. Annabi ya koma Madina da zama bayan an aiko shi Manzon ƙarshe a daidai shekara ta goma da karɓar Manzanci. A halin yanzu, Musulmi suna ƙirga shekarunsu ne daga shekarar hijirar Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, zuwa Madina. A Madina ne Allah ya ƙarasa saukar da Manzanci ga Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, shari'a ta kammala sosai.

Nasabar Manzon Allah,
Sallallahu Alaihi wa Sallama, mai Girma

Shugabanmu Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, shi ne Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, ɗan Abdullahi ɗan Abdul-Muɗɗalib ɗan Hashim ɗan Abdul Manafi ɗan Kusayyu ɗan Kilabu, shi ne Hakimu ɗan Murrata ɗan Ka'abu ɗan Lu'ayyu ɗan Galibu ɗan Kahru ɗan Maliki ɗan Nadari ɗan Kinanata ɗan Khudaimata ɗan Mudrikata ɗan Iliyasu ɗan Mudari ɗan Nizari ɗan Ma'aɗɗi ɗan Adanan wanda nasabarsa take tuƙewa zuwa ga Sayyadina Isma'il ɗan Annabi Ibrahimal-Halil, tsira da amincin Allah su tabbata a gare su.

Mahaifiyarsa ita ce, Aminatu 'yar Wahabi ɗan Abdi Manafi ɗan Zuhrata ɗan Kilabu, shi ne Hakimu kaka na biyar ga Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama.

Kuruciyarsa da Wasu Halayensa

Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya zamanto tun tashinsa yana nisantar yin wasanni da jin daɗi, ga shi da yawan ƙana'a da juriya, ba ya bayyanar da halin da yake ciki. Tun yana yaro ba ya magana sai ta gaskiya, kuma shi mafi girman mai riƙe amana ne, mai kuma nisantar maganganu marasa kyau. Ga shi da cikar muruwa da kamala, mai kyakkyawar hulɗa, mai haƙuri mai kaifin basira.

Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, ya fi kowane irin mutum girman daraja a wurin Allah domin dukkan halayensa da ɗabi'unsa *Alƙur'ani* ne. Ba ya yin magana ta son zuciya, ko saurin hushi ko gwale mutane, ballantana ya zage su. Annabi shi ne mafi girman daraja a duniya, duk da haka shi mai son jama'a ne mai ziyartarsu a gidajensu a halin lafiya ko rashin lafiya. Yana kuma zuwa jana'iza, yana son matalauta da miskinai, yana zama tare da su. Shi ke ɗaukar abin zubo sayayyarsa ko cefanensa zuwa kasuwa da kuma in ya dawo, ba shi da girman kai, yana girmama talakawa da mawadata. Yana saurin fara sallama ga wanda ya haɗu da shi a kan hanya, da ba shi hannu a gaisa, yana zuwa gayyata idan an yi masa. Ya zamanto yana wanke tufafinsa da kansa, yana tatsar madara daga tunkiya da kansa don ya sha, yana yi wa kansa hidima ba tare da nuna damuwa ba.

Yana taimakon jama'a a kan buƙatunsu, ba ya yi wa mutane baƙar magana idan ya zauna tare da su a mazauni ɗaya, yana girmama su. Ba ya guje wa jama'a, ba ya fara tashi ya bar su, ba ya tsinke wa mutane zance, ko ya yi musa katsalanda ko ya tsoma baki kan abin da bai shafe shi ba, duk ba ruwansa da yin haka. Yakan tambayi abokin zama da bai gan shi ba na tsawon wani lokaci. Annabi, sallallahu alaihi wa sallama, ba ya cutar da kowa, ba ya yi wa kowa wani karen aiki ballantna ɗanyensa. Shi mai saurin yafewa ne ga abin da

aka yi masa da mantuwa ko da isgili ko da gangan ko a kan sani, ba shi da riƙo a zuciyarsa. Da ɗai bai taɓa dukan (bugun) wani abu da hannunsa ba, sai a yayin jihadi. Yafi kowane mutum alheri da kyautata wa mutane da ƙoƙarin inganta rayuwarsu. Annabi, sallallahu alaihi wa sallama, ba marowaci ne ba, mai yawan kyauta ne, mai baiwa ne, mai karimci ne. Mai yawan ambaton Allah ne (zikiri), ba ya tsoron kowa sai mahaliccinsa Allah, domin haka, ba ya jin shakkar bi ta cikin abokan gabarsa shi kaɗai, don ya san ba abin da za su iya yi masa, Allah shi ne mai kare shi. Annabi yana ziyartar maƙabartu, ya yi wa mamata addu'a, ya nema masu gafara. A kullum yana sake da fuska, mai fara'a ne, mai son jama'a, mai yin farat-farat da su, muddin dai ba a kauce wa wani abu na shari'a ba.

Renonsa da Tarbiyyarsa da Kiran sa,
Sallallahu Alaihi wa Sallama

Duniya ta haskaka da zuwan Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, abubuwa suka sassake, ya buɗe abin da ya kasance a rufe, cikamakin abin da ya rigaya, mataimakin gaskiya da gaskiya, mai shiryarwa ga tafarki madaidaici. Muna yin maraba da zuwan shugabanmu Annabi Muhammadu da cewa:

Maraba da kai Muhammadu ɗan Amina,
Maraba da shugaban duka Annabawa.
Muhammadu sabulu mai wanke dauɗa,
Muhammadu magani mai warke kowa.
Muna zuba godiya ga Ubangijinmu,
Da ya aiko ka domin kyautatawa.
Gaba ɗaya mui salati gun Muhamman,
Mabuɗin duk abin da ka rurrufewa.

Muhammadu ya taho domin bayani,
Ya miƙe duk abin da ka rikirkicewa.
Da kalmar gaskiya ya taho gare mu,
Ya taimaki gaskiyar da ka karkacewa.
(*Imam, 1975 :35)*

Tarbiyyar Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ta fara ne tun daga mahaifiyarsa Aminatu, farkon wadda ta rene shi, mahaifinsa Abdullahi ya rasu tun yana ciki. Daga nan aka ba da shi reno a ƙauye ga Nana Halimatus Sa'adiyya. Shaima'u 'yar Halimatu, sai tana yi wa Annabi tawai tana cewa:

Ya rabbana abƙi lana Muhammada,
Hatta narahu yafi'an wa'amrada.
Summa narahu sayyidan musauwada,
Waƙbit a'ada'ihi ma'an wal-hussada.
Wa'adi̓ihi izzan yadumu abada,
Wahtimlahu bil hairi was sa'ada.

Mala'iku sun tsaga ƙirjinsa suka cire gudan jinin zuciya da ke sa yin laifi. Bayan Halimatu ta dawo da shi Makka, lokacin yana da shekaru huɗu, mahaifiyarsa Aminatu ta rasu, sai ya koma hannun kakansa Abdul-Muɗɗalib, bayan rasuwarsa, sai ɗansa Abu Ɗalib ya ɗauki renonsa yana a matsayin baffansa. Annabi ya tashi da halaye masu kyau, mai gaskiya, mai amana, ba a haɗa kai da shi a yi zalunci. Kafin saukar masa da Annabci ya taɓa kasuwanci da kiwon dabbobi, sannan ya auri Nana Khadijatu. Bayan da Annabci ya sauka a kansa, lokacin yana da shekaru arba'in, ya fara kiran 'yan'uwansa, sai maƙwabtansa, da garinsu Makka, daga nan har ya fita waje. Mala'ika Jibrilu shi ne mai zo masa da wahayi.

Ya yi yaƙe –yaƙe na jihadi da abokan gaba, har addinin Musulunci ya tsayu sosai da taimakon Sahabbansa.

Abubuwan da Manzon Allah ya zo da su

Kiran Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, ya zo wa duniya da abubuwa sababbi kamar haka:

- Kaɗaita Allah shi ɗaya wanda bai da abokin tarayya ko cuɗanya. Allah kawai shi ne abin yi wa bauta, bai da abokin gunki.
- Hisabi da ranar Tashin Kiyama. Za a bayyana wa mutum ayyukan da ya yi don yi masa sakamako kan haka.
- Littafin Allah saukakke wato *Alƙur'ani* mai tsarki. Wahayin da Jibrilu yake saukar wa Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, daga wurin Allah shi ne ya haɗa *Alƙur'ani*.

'Ya'yan Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa Sallama

Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, ya haifi 'ya'ya guda bakwai, uku maza, huɗu mata, su ne kuwa kamar haka:

Daga cikin maza akwai:
Sayyadina Alkasim

Sayyadina Abdullahi

Sayyadina Ibrahim

Daga cikin mata akwai:
Sayyada Faɗimatu (Zahra'u)

Sayyada Zainabu

Sayyada Ruƙayyatu

Sayyada Ummu Kulsumi

Dukkan waɗannan ‘ya’ya nasa sun fito ne daga ɗakin matarsa Nana Khadija, sai Ibrahim wanda ya fito daga ɗakin Nana Mariyatal Kibɗiyya.

Matan Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa Sallama

Annabin Rahama, Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, ya auri matan aure guda goma sha ɗaya (11), wata bayan wata waɗanda suke kamar haka:

Nana Khadijatu
Ramlatu
A’ishatu
Hafsatu
Saudatu
Maimunatu
Zainabu
Safiyyatu
Hindu
Zainabu[44]
Juwairatu

Wasu Dangin Manzon Allah,
Sallallahu Alaihi wa Sallama

Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, yana da baffofi da kaworabe maza har guda goma sha ɗaya (11), biyu (2) daga cikinsu sun Musulunta su ne, Hamzatu da Abbasu. Kaworaɓensa mata kuwa shida (6) ne, uku (3) daga cikinsu suka Musulunta, su ne: Safiyatu da Atikatu da Arwa.

[44] Wato Uwar miskinai, Ummul Masakin.

A ƙarƙashin Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, kuma akwai huddamu wato masu yi masa hidima, ko hadiman addinin Musulunci, guda ɗari da saba'in (170). Daga cikinsu akwai Anas da Mariyatu da Ummu Aimana.

Abubuwan da Manzon Allah,
Sallallahu Alaihi wa Sallama, ya Keɓantu da su

Daga cikin abubuwan da Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya keɓantu da su akwai waɗannan:

- Kasancewarsa Annabi kuma Manzon ƙarshe.
- Kasancewarsa Mafificin Manzanni da Annabawa.
- Shi ne ƙasa za ta fara tsagewa ta buɗe masa ya fito, bayan an yi busar tashi.
- Shi ne zai fara shiga Aljanna.
- Shi ne wanda zai yi ceto.
- Shi ne za a karɓi cetonsa kawai.
- Shi Manzon Allah ne zuwa ga mutane da aljanu.
- Zuciyar Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ba ta yin barci.
- Yana ganin abin da ke bayansa.
- Yana gani a cikin kowane irin duhu.
- Jikinsa ba ya nuna inuwa.
- Kudaje ba su sauka a kan jikinsa.
- da sauransu.

Wasu Ɗabi'un Manzon Allah,
Sallallahu Alaihi wa Sallama

Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, ya zamanto mutum ne mai yawan son sanya turare a jikinsa da tufafinsa da muhallinsa. Yana ƙin wari, ko wani abu maras daɗi, yana sanya kwalli a idanuwansa, shafawa sau uku da macci, musamman ma a ranekun Juma'a. Ya yi saye da sayarwa da fatauci, da sauran hulɗodin cinikayya. Ba ya son yawaita cin abinci, ko ya ci abinci har ya cika ya tumbatsa. A ƙarshen rayuwarsa yakan tanadar wa iyalinsa abincin da zai kai su har shekara ɗaya. Yana mayar da hankali sosai ga duk aikin da ya sa a gaba. Yana rayar da darensa da salloli da zikiri har wata rana, sai kafafunsa sun yi nauyi, sun kumbura saboda tsayuwa a wajen yin raka'o'i. Sayyada A'ishatu takan ce masa, "Yaya za ka tsananta wa kanka, bayan Allah ya gafarta maka". Yakan mayar mata da amsa ta cewa "Ashe ba zan zama bawa mai godiya ga Ubangijinsa ba". Annabi, sallallahu alaihi wa sallama, yana karɓar Hadiyya, amma yana mayar da Sadaƙa. Mafi yawancin addu'arsa ita ce:

> *"Allahumma ya musabbitul-Kulubi, sabbit ƙalbi ala dinika",* Ya Allah mai tsayar da zukata, ka tabbatar (tsayar) da zuciyata a kan addininka.

Buhari ya ruwaito, "Allah ya ba kowane mutum rabonsa na halaye da ɗabi'u, kamar yadda ya rarraba arziki ya ba kowa nasa. To Annabi, sallallahu alaihi wa sallama, ya fi kowa samun ɗabi'u cikakku, kyawawa kuma tsarkakakku. Ya fi kuma kowa gurabu maɗaukaka, da ake ƙauna, kuma kowa yake yarda da su. Allah ya tara wa Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, kyawawan ɗabi'u, da su ya yi amfani wajen siyasar tafiyar da Larabawa da suka zama kamar dabbobin daji barkatattu kuma ruɗaɗɗu. Ya yi haƙuri a kan al'adunsu na ƙauyantaka, har suka yaƙi iyalin

abokansa[45] da aminansa waɗanda suka yarda da shi, suka yi hijira suka bar gidajensu. Annabi ya tashi a tsakanin jahilan mutane yana maraya, ba shi da uba, mahaifiyarsa ma ta rasu daga bisani, sai dai ya tashi a hannun 'yan'uwa, makusanta. Allah ya sanar da shi kyawawan ɗabi'u da mafifitan halaye, sai ya zauna da su cikin juriya, har sai da ya sa suka fahimci shari'ar Allah da godaben Allah madaidaici. Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, da kansa yana cewa, "Ubangijina ya yi mini ladabi, kuma ya kyauta yin sa"[46]. Daga nan ya kasance mafificin mutane sanin kyawawan halaye.

Wasu Daga Cikin Mu'ujizojin Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa Sallama

Wasu daga cikin mu'ujizojin Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, su ne:

- *Alƙur'ani,* mai girma wanda mutane da aljanu suka kasa kawo ko da aya guda ɗaya irin wadda take a cikinsa.
- Tsagewar wata a daren goma sha huɗu, dare da ya fi kowane dare haske, ya faɗo a tafunan hannuwansa, masu tsarki, sallallahu alaihi wa sallama.
- Ɓuɓɓugowar ruwa daga tsakanin yatsun hannuwasa masu daraja a wuri busasshe, wato faƙo da ba shi da alamun samun ruwa, har sai da dukkan mayaƙa suka sha ruwa suka ƙoshi, sannan suka yi alwala.
- Ciyar da mutane fiye da dubu daga abincin da aka yi da garin da bai wuce mudu ɗaya ba.

---

[45] Musamman ma Sahabi Abubakar Siddiƙu, Allah ya yarda da shi, da sauran waɗanda suka yi imani da shi a farkon kira na Musulunci.
[46] Wato "Addabani Rabbi fa'ahsana ta'adibi"

- Duwatsu da itatuwa suka yi magana da shi, suka gaya masa damuwarsu.
- Kukan gindin dabino yana nuna kwaɗayinsa da shauƙinsa ga Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, saboda ya daina gincirawa a wajensa, har sai da kowa ya ji kukansa. Bisa haka, Manzon Allah ya ba shi haƙuri.
- Tasbihin tsakuwa da ke a tafin hannunsa.
- Mayar wa da Kattadatu idanuwansa, ya koma yana gani sosai har fiye da da.
- da sauransu da yawa.

Fasahar Harshen Manzon Allah,
Sallallahu Alaihi wa Sallama

Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, ya kasance mafifcin halittun Allah fasaha, da iya magana da kaifin zance. Akwai daga cikin fasaha da balagar zance na Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, waɗannan maganganun kaifafa tunani da suka haɗa da:

-Mutum yana tare da wanda yake so[47].

-Mai baban rabo shi ne wanda ya wa'azantu (shiryu) da waninsa.

-Niyyar mumini ta fi daga aikinsa.

-Yaƙi dabara ne, ko yaƙi yaudara ne[48].

[47] Wato "Almar'u ma'a man ahabba'.
[48] Wato "Alharbu Khud'atun'.

-Mai tsanani ba shi ne wanda ya galabaici mutane ba, a'a mai tsanani shi ne wanda ya rinjayi (son) kansa.

-Labari bai kai kamar gani da ido ba.

-Bala'i rataye yake da salo (mai wayo shi bala'i ke faɗawa).

-Kunya alheri ce dukkanta[49].

-Duk wanda ba shi da kunya, sai ya aikata abin da yake so[50].

-Yasasar rantsuwa tana risbe gidaje[51].

-Shugaban mutane shi ne hadiminsu (bawansu).

-Lafiya da samun sarari, ni'imomi ne guda biyu ga bawa.

-Ku nemi taimako a kan buƙatunku cikin ɓoyewa da sirrantawa, haƙiƙa, kowane ma'abucin ni'ima abin yi wa hassada ne[52].

-Wanda ya yi mana algussu ba shi tare da mu[53].

-Wanda ya yi nuni a kan alheri kamar ya aikata shi ne[54].

-Zama ma'abucin wadatuwa (ƙana'a) mutane za su ƙara son ka.

-Ko ba ku iya yalwata wa mutane da dukiyoyinku, to, ku yalwata musu da kyawawan halaye.

-Munanan halaye suna ɓata aiki, kamar yadda rina ke ɓata zuma

---

[49] Wato 'Alhaya'u kulluha khairun'.
[50] Wato 'Iza lam tastahyi fasna'a ma shi'ita'.
[51] Wato 'Yaminul fajirati tada'ul biladi baladiya'.
[52] Wato 'Kullu zi ni'imatin mahsudun'.
[53] Wato 'Man gasshana falaisa minna'.
[54] Wato 'Man dalla ala khairin kafa'ilihi'.

-Ana auren mace don kyawonta, ko dukiyarta ko addininta to, ka riƙi ma'abuciyar addini za ta tanade ka a lokacin talauci.

-Kana'a dukiya ce, ba ta ƙarewa, kuma taska ce wadda ba ta ƙarewa.

-Tattali a wajen ciyarwa, rabin rayuwa ne, kyawawan tambayoyi rabin ilmi ne, natsuwa a wajen mutane rabin hankali ne.

-Wanda ya yi Istihara ba zai taɓa taɓewa ba, wanda ke shawara kuma ba shi tare da nadama.

-Wanda ya yi tattali (tsimi da tanadi) ba shi talauci.

-Musulmi shi ne wanda ya tsira da harshensa da hannunsa. Mai hijira kuwa shi ne wanda ya ƙaurace wa haramun da sauran ɓarnace-ɓarnace.

-Ka tsare amana ga wanda ya ba ka ita, kada ka cuci wanda ya amince maka.

-Tarbiyya (rainon rai) tana canja ɗabi'a.

-Mai neman ilimi da mai neman duniya ba su ƙoshi.

-Ku riƙi arziki daga doron ƙasa, ku yawaita noma.

-Kada ka bayyana shammata ga ɗan'uwanka saboda wata cuta da ka lura yana tare da ita, sai Allah ya warkar da shi, kai kuma ya jarabce ka da ita.

-Kowane irin aiki, sai da niyya[55].

-Neman hujja tana ga wanda ya yi kuka (ƙara), amma rantsuwa tana ga wanda ya yi musu.

---

[55] Wato 'Inna mal a'amali binniyati'.

-Halal da haram a bayyane suke[56].

-Imanin mutum ba ya cika, sai ya so ga ɗan'uwansa abin da yake so ga kansa[57].

-An rataya wa zukata son wanda ya kyautata zuwa gare su, da ƙin wanda ya munana zuwa gare su (zukata).

-Wanda ya yi shiga (kamancewa) da mutane yana cikinsu[58].

-Ku jiƙan wanda ke a ban ƙasa, wanda ke a sama (Allahu) zai yi muku rahama (ya kuma yi jinƙai a gare ku)[59].

-Yana daga cikin cikar Musuluncin mutum barin (ƙin shiga) harkar da ba ta shafe shi ba[60].

-Ana son ɗan'adam ya taƙaita wa kansa cin abinci, ya kasance ya kasa cikinsa gida uku, kashi na ɗaya, ya zama na abinci ne, kashi na biyu, shi kuma na ruwan da zai sha, sai kashi na uku da zai zama don yin numfashi. Manzon Allah, sallallahu alaihi wa wa sallama, ya ce: "Ya fi kamata ga mutum ya dinga yin loma uku kawai a cin abincin lokaci ɗaya, kamar shi, sallallahu alaihi wa wa sallama, yadda yake yi".

Wafatin Manzon Allah,
Sallallahu Alaihi wa Sallama

Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya yi wafati ranar Litinin sha biyu (12) ga watan Rabi'ul Auwal a cikin shekara ta goma sha ɗaya da hijira zuwa Madina. Ya tafi ga

---

[56] Wato 'Inna mal halalu wal-haramu bayyinun'.
[57] Wato 'La yuminu ahdukum hatta yuhibbu li'ahihihi ma yuhibbu linafsihi'.
[58] Wato 'Man tashabbaha biƙaumin fahuwa minhum'.
[59] Wato ''Irham man fil'ardhi, yarhamukum man fissama'i'.
[60] Wato 'Min husnil islamil mar'i tarkuhu mala ya'anihi".

jinƙan Allah a lokacin da yake da shekaru sittin da uku a duniya. A wannan rana Sahabai da sauran jama'ar Musulmi suka yi matuƙar juyayi ƙwarai, suka nuna damuwarsu a kan haka. Sahabi Abubakar, Allah ya yarda da shi, ya yi wa Musulmi jawabi ya ce:

> "Ku saurara wanda ya kasance yana bautar Muhammadu, sallallahu alaihi wa wa sallama, to, ya tafi zuwa ga jinƙan Ubangijinsa. Kuma wanda ya zamanto yana bautar Allah ne, to, yana nan a raye, ba ya mutuwa".[61]

Wannan zance na Sahabi Abubakar shaida ce mai tabbatar da Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya yi wafati.[62]

---

[61] Wato 'Man kana ya'abudu Muhammadan fa'inna Muhammadan ƙad mata, waman kana ya'abudullah, fa'innallaha hayyun layamutu'.
[62] Allah ya tara mu baki ɗaya da su a Darul-salam, amin.

5

SASHEN WAƘOKIN KOYAR DA IBADA

Waƙa tana ɗaya daga cikin hanyoyi mafi sauƙi wajen isar da saƙo zuwa ga mutane, kuma su yi saurin gane shi kuma su haddace shi. Domin haka aka rubuta waɗanan waƙoƙi don su koyar da mutane wasu dangogin sha'anin ibadarsu da sauran hukunce-hukuncen shari'a. An keɓe wannan sashi inda aka zo da wasu waƙoƙi masu koyar da ibada a addinin Musulunci kamar haka:

Waƙar Tallafi

Da sunanka Allahu mai luɗɗufi,
Ka ba mu basira cikin izzifi.

Salati, salami ga Almusɗafa,
Muhammadu Shumagaban tallafi.

A ya ɗaliban hafizal fa'ida,
Ku dage ga *Kur'ani* mai haddafi.

A ya haliƙinmu muna addu'a,
Mu sami karatu cikin luɗɗufi.

Ka ba mu fahimtarka ya Auwalu,
Mu gane karatunmu ba sa'afi.

Mu sabunta sunanka ya Ahiru,
Mu gane karatunmu ba hassafi.

A ya malamanmu muna addu'a,
Ku daure halinmu cikin waƙƙafi.

Idan munka ɓata ku yafe mana,
Akwai rai da laifi cikin shaggafi.
Idan munka gyara ku gode mana,
Ku ɗauke mu almajiran tallafi.

Muna jin du'a'inku ya ɗalibai,
Ku daure zuwanku cikin zarrafi.

A ya ɗalibai, 'yan'uwa, gafara,
Ku daina jidali fa sai kun tafi.

Muna yin kira gun iyaye duka,
Ku turo ɗiyanku su bar waƙƙafi.

Muna bayyana muku madda duka,
Hadisi da *Kur'an* cikin tallafi.

Ibada da sirar ma'aiki duka,
A wannan dirasa ta yi tallafi.

Muna godiya har iyaye duka,
Kuna tsare aikinku har mu tafi.

Ku san malami mai tsaron gaskiya,
Ya shiryar da yara cikin luɗɗufi.

Muna ƙoƙari babu alfahari,
A koyar da yara cikin tallafi.

Muna godiya gunka ya Rabana,
Ka ƙaro basira ta yin tallafi.

A ya Rabbana, Rabbana, Rabbana,
Ka sanya mu aljanna ba waƙƙafi.

5/2/1413 H.
3/8/1992 M.

Waƙar Tariyar Baƙi daga Ɗalibai

Allah, Allah, Muhammad Rasulullah,
Allah, Allah, Muhammad Rasulullah.

Mun sallama, salamu alaikum,
Mun gaishe ku, muna daɗa ƙarawa.

Sunan Allah, kana sunan Manzo,
Su muke kullum riƙa farawa.

Mu ɗaliban fagen *Kur'ani* ne,
Koyo muke muna ta karantawa.

Uwa ɗaya, uba ɗaya duk tare,
Da mu da ku ba ma iya warewa.

Domin Allah domin girman Manzo,
Ku taimaka domin daɗa ƙullawa.

Fata muke in kun gama duba mu,
Ku yi addu'a Allah daɗa buɗawa.

Mu ma a nan fata muke kullum,
Allah ya sa ku zam daɗa jurewa.

Amma ku san mu masu biyayye ne,
A gare ku don ba ma iya fasawa.

Allah ya mai da ku gidajenku,
Da lafiya da ƙarfin dawowa.

Allah gwani Allah Sarki, Jallah,
Mun godiya muna daɗa godewa.

Waƙar Gane Ubangiji

Mu muna son Ubangiji,
Rabbana mai gani da ji.

Ya Ilahi Ubangiji,
Mai halitta aji-aji.

Ya yi sammai da girgije,
Ya yi ƙassai Ubangiji.

Ya yi rana kaza wata,
Yai itace Ubangiji.

Yai mutane fa 'yan'adam,
Ya yi dabba Ubangiji.

Ya yi kogi da tsaunuka,
Ya yi ƙwari Ubangiji.

Sai mu bauta wa Khaliƙu,
Ban da shi ba Ubangiji.

Mui salati da sallama,
Gun masoyin Ubangiji.

Musɗafa wanda ac cikon,
Annabawan Ubangiji.

Waƙar Yarda da Musulunci

'Yan'uwana duk ku taho mu bi,
Islam addinin gaskiya.

A cikin addinai ba kamar,
Islam addinin gaskiya.

Musɗafa ya zo shi ya kammala,
Islam addinin gaskiya.

Duka al'umma an ce su bi,
Islam addinin gaskiya.

Larabawa, Turawa ku bi,
Islam addinin gaskiya.

Jamus da Faransa ku zo mu bi,
Islam addinin gaskiya.

Indian, Pakistan duk ku bi,
Islam addinin gaskiya.

Hausawa, har Igbo ma mu bi,
Islam addinin gaskiya.

Yarbawa duk ku taho mu bi,
Islam addinin gaskiya.

Dukkanmu mu zo mu haɗe cikin,
Islam addinin gaskiya.

Ba bambanci a ciki nasa
Islam addinin gaskiya.

Ni ina fahari da nake cikin,
Islam addinin gaskiya.

Waƙar Matakan Addinin Musulunci

Amshi: 'Yan'uwa ku taho ku saura,
ra ga waƙa mai hidaya.

Rabbi mun roƙe ka Allah, Jalla ba mu yawan hidaya.
Mun Salati da sallama gun, Musɗafa Manzon hidaya.
Ɗalibai ne masu ƙaunar, Allubabbiyar hidaya .
Nan muke koyo da ilmi, Don mu ɗau hanya ta manya.

Fiƙhu, Tauhidi da Salla,
Sai cikon na biyar Siyami,
Mun yi imani da Allah,
Sa da Manzanni da littaf,
Ƙaddara ce mai fa kyau ce,
Mai gani mai ji Ta'ala,
Ga Mala'ikku na Allah,
Shugaba Jibrilu ne shi,
Masu kaɓar rai gaba ɗai,
Mai ƙahon Tashin Ƙiyama,
Sai mu zo gun Mursalina,
Nuhu, Ibrahim da Musa,
Sa da ɗan Maryam Isa,
Kun ga littafan Ta'ala,
An yi Attaura da Linji,
Mallakinsu gaba ɗayansu,
Al-Huda, *Kur'anu*, Nurun,
Kun ga sallolin farilla,
Assuba, Zuhrin, La'asar,
Asuba raka'a guda biyu,
Azzuhur, La'asar guda huɗu,
Magriba raka'arta ukku,
Babu inganci ga sallah,
Malamai masana shari'a,
Sun gaya mana babu salla,
Kun ga alwalla siffarta,
Wanke hannaye da farko,
Sai a shaƙa sai a fyace,
Wanke hannaye zuwa gwi,
Shafa kai shafa ga kunne,
Jalla Sarki taimake mu,
Har mu zam ɗa'a ga Manzo,
Har mu zam ɗa'a ga walid,
Shugabannin Muslimina,
Hajji, Zakka in da hanya.
Ne shika-shikan hidaya.
Har Mala'ikunsa gaya.
Fai da Ranar Alƙiyama.
Har maras kyau mun biyayya.
Mai kalami Wahidiyya.
Za mu zana wansu manya.
Sa da Mika'il ƙidaya.[63]
Karƙashin Azra'iliyya.
Sai mu ce Israfiliyya.
Annabawa manya-manya.
Ya Kalamullahi manya.
Sai Muhammadu[64] mai hidaya.
Su guda huɗu manya-manya.
La, Zabura don hidaya.
Shi ya tara dukan hidaya.
Anka ba Manzon hidaya.
Su biyar ne ga ƙidaya.
Magriba, sallar Ishaya.
Su ake yi rak'atayya.
Biu da biu su ne nihaya.
Sai huɗun sallar Ishaya.
Sai da alwalla da niyya.
Masu ihlasi ga niyya.
Sai da alwalla fiyayya.
Za mu nuna don a koya.
Kurkurewa na biyayya.
Wanke fuska mai da niyya.
Wa ta hannun mirfaƙayya.
Sai ƙafafu, rijjiliyya.
Sa mu zam ɗa'arka gaya.
Musɗafa jigon hidaya.
Danmu ne tushen hidaya.
Duk mu karɓa mui biyayya.

---

[63] Wato 'Mala'ikan mutuwa wanda aka fi kira da Mala'ika Azara'ilu'.
[64] Sallallahu alaihi wa sallama

Nan fa waƙar za ta ƙare, Arba'in ne sa ƙidaya.

Waƙar Kabari

Amshi: Ni ba abin da nake haufi,
Sai rad da za a saka kabri.

Ni ba abin da nake tsoro,
Wurin da za a haƙa taro,
Shi babu faɗi sai tsoro,
Daidai tsawon kowa kabri.

Shi babu wanda ya zarce shi,
Kuma babu mai iya kore shi,
Haka ba dibarar ture shi,
Wanne ku san shi ne kabri.

Ku mutum da ya kwanta ciyyo,
Ɗiya da mata sai wayyo,
Kowa ya koma ba wayo,
An tabbata yau sai kabri.

In anka ce mutuwa ga ta,
Ta bayyano maka harshenta,
Ta gama da bawa aikinta,
Sai tattalin tonon kabri.

Sai 'yan'uwanka su dage ma,
Wanka na gawa za sui ma,
Sannan su sanya lufafar ma,
Liman da yai salla kabri.

Taron maƙwabta duk ga su,

Da waɗanda anka biɗo ga su,
Da waɗanda sunka jiya ga su,
Su za su kai shi cikin kabri.
Aikin da kay yi cikin dunya,
Hairi da sharri duk ga ya,
Ya zame gare ka abin juya,
Ya taya ka yauci cikin kabri.

Sallarka in kai kyakkawa,
Ta taho ta ɗebe ma kewa,
Albarkacinta ka sha baiwa,
Sannan a buɗa ma kabri.

In ka yi salla mummuna,
Ita za ta sanya ma rafkana,
Sannan da kuka ga ƙuna,
Kuma dai a ƙara matse kabri.

Kaiconka wawa mai kuɗɗî,
Bai fid da zakka har tukɗî,
Don dukiyar nan tai fadî,
In ya mace shi ɗai kabri.

Farkonka an yi ka ba sisi,
Kuma babu komi sai gasi,
Yau ga ka ka zam mai hausi,
Ka mance komawa kabri.

In anka sa ka cikin rame,
Laka da ganye za su zame,
Daurin itace sai a kume,
Wannan kushewa ce kabri.

Bayan mutane sun kai ka,
Sun wanke hannu sun bar ka,
Kowa ga hanya sai kuka,
Tausan barin ka cikin kabri.

Kowansu ya zo ya zauna,
Ya kama kuka don ƙuna,
Rabuwar aboki in an tuna,
Shi ɗai cikin ramen kabri.

In an rufe ka an juya,
In an gusa da matambayya,
Kai ɗai su yo maka tambayya,
In ka amsa ni'imar kabri.

In ko kana yin ɓatutta,
In anka ce me kai bauta,
Ko ko a ce me ka kaɗaita,
In kai shuru kulkin kabri.

Kabri ciki nai ba mota,
Ba shugaba ciki ba tuta,
Ko ko sihani ba buta,
Balle shira'i cikin kabri.

Shi ne msaukin mai hali,
Shi ne masaukin alƙali,
Shi ne masaukin 'yan koli,
Har 'yan sharu sa 'ya'yan kiri.

‘Ya’ya na sarki duk sa su,
Sarkin da fadawa sa su,
Barwa da bayi duk sa su,
Karshensu ramen nan kabri.

Ulama’u malamai duk dai,
Kirga su masu biya daidai,
Kowa ka sa shi ciki daidai,
Don kar a bar kowa kabri.

Juhala’u su ne jahillai,
Gufala’u su ne gafillai,
Buhala’u su ne bahillai,
Duk dai akwai su cikin kabri.

Manyansu soja da yaransu,
‘Yan sanda su da mobayilsu,
‘Yan kwastan su da iyalinsu,
Kowa ka sa shi cikin kabri.

Ni ma da ke fasalin rame,
Wallai ku san sai mun kome,
Duk babu mu duk an kame,
Duk mun shige a cikin kabri.

Ku ma da ke amshin waƙe,
Da mazan da mata ba noƙe,
Ka cire tababa bar tarke,
Wata rana sai a cikin kabri.

Allahu ya yi ka yai ranka,
Sannan ya yo ka mutum kanka,
Kai ƙoƙari ka tsare kanka,
Daga tanadi na duhun kabri.

Duk sai mu tashi mu tirtirje,
Aikin na Manzo mu gaggaje,
Mu zame koyi ku mu daddarje,
Sai ko mu sam hasken kabri.

In anka ce wa yat tsara,
Shi ne Sa'idu uban Zahra,
Da Anas da Hindatu duk ƙara,
Ummi, Umamatu kai nazri.

Ga uwar Rahina nak karɓa,
Ka haɗa da Fadîma ba saɓa,
Ita ce fa Larai ba laɓaɓa,
Ƙanwa ga Lubabatu mai haƙri.

Liti na rana talatinta,
A wata na Augas yay yo ta,
A alif cas'in sa ukkunta,
Uba na Yusha'u yai tsari.

Waƙar fa duk in ka duba,
Layinta hurhuɗu ba babba,
Baiti talatin anka zuba,
A cikin wannan tsarin kabri.

13/03/1414 A.H.
30/08/1993 M.

Waƙar Tuni da Ranar Tashin Kiyama

Alhamdu lillahi mun ta gode Ubangiji,
Da ya ba mu iko don mu sam ƙofar fita.

Ku mu daina guri kar mu zam son zuciya,
Kuma ban da girman kai mutum in ka fita.

Ranar fita daga duniya ba mai gudu,
Rannan maɗauka rai ba za fa su dakata.

Ba za su nuna ko kaɗan sun san ka ba,
Aikinsu ɗaukar rai a ranar ba kwata.

Horo nake ga mutum ya gane duniya,
Don kar ya zauna har ya san daɗi nata.

In anka ɗauke ranka ka gama ayyuka,
A kai ka baƙunta gida mai ƙuntata.

A cikinsa shi kam babu haske sai duhu,
Rannan uƙuba ba wurin tsere mata.

Amma idan ka zam mutum mai hankali,
Dukkan azaba za ka kakkauce mata.

Lallai gare ka Mala'ikun rahama suke,
Su yi ma bishara kan shiga Aljannata.

A wajen fitar rai za su rangwanta maka,
Kan hankali za sui, su kai ma'aji nata.

In ko ka zanto mai baƙaƙen ayyuka,
To, za su fizgo ranka ba tausai nata.

Tashin Kiyama in ya zo ka sha wuya,
Sai an tuna maka ayyukan da ka aikata.

Bakinka yai nauyin faɗi ran gaskiya,
Gaɓɓai a ranar ne kawai kan ambata.

Rannan fusaku kan yi haske ko baƙi,

Daidai da aikin wanda duk ya aikata.

Kowa a rannan hankali zai birkice,
Sai wanda Allah yaj jiƙai ba ya ɓata.

Allahu mun roƙe ka kai mana tallafi,
Ka yi wa Musulmi dukkani mun ambata.

Domin dalilin Annabinka Muhammadu,
Mun roƙi haske wanda yaf fi farin wata.

6

SASHEN WAKOKIN YABO DA BEGEN MANZON ALLAH, SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAMA

A wannan ɓangare za a kawo waƙoƙin da aka rubuta kan yabon Manzon Allah, Annabin Rahama, Muhammadu, Cikamakin Manzanni, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Waƙoƙin da aka zo da su sun haɗa da:

Waƙar son Manzon Allah, Sallallahu Alaihi wa Sallama

Manzon Allah ina son sa,
Domin Allah yana son sa.

A cikin sammai ana son sa,
A cikin ƙassai ana son sa.

Da Mala'iku suna son sa,
Duk talikai suna son sa.

Da mutane ma suna son sa,
Mata da maza suna son sa.

Sannan manya suna son sa,
Haka ma yara suna son sa.

Mai son Allah yana son sa,
Mai ƙin Allah yana ƙin sa.

Ya dace wanda ke son sa,

Ya taɓe wanda bai son sa.

Aljanna ga wanda ke bin sa,
Da wuta gun wanda bai bin sa.

Waƙar ya Rabi Salli ala Almusɗafa

Amshi:Ya Rabbi Salli ala Almusɗafa,
Annabinmu wanda ba ay yo kamarsa ba.

Allah ina miƙo gaisuwa ga kai,
Na tabbata Allah ba kamar ya kai,
Ko cikin mutum ko aljan ba ya kai,
Taimake mu Allah ba don halinmu ba.

Na gai da Manzon Allah shugaba,
Shugaban halitta Manzo Mujittaba,
Allah ka ƙara karama ga shugaba,
Annabinmu wanda ba ay yo kamarsa ba.

Allah ka ba mu fasaha mu wallafa,
Waƙa cikin darajar Almusɗafa,
Manzo Rasulu Habibi Musɗafa,
Mui yabon Habibu karimi shugaba.

Zahiri haƙiƙa ƙauna ta isa,
Ta cika mu fal har tamkar ta fasa,
Roƙo muke yi Allah kar ka sa,
Mui ragin yabon Manzona shugaba.

Kullum dare, rana ko safiya,
Ambato muke yi sosai ka jiya,

Sassan jikinmu sunai har jijiya,
Albarkacinsa muke so shugaba.

Kalma ta baki haƙiƙa tai kaɗan,
Komai mutum zai ce yau yai kaɗan,
Sai dai kawai a taɓa ko da kaɗan,
Ba wai a kai ƙarshe kan yin sa ba.

Duniya ku san an yo dominsa ne,
Lahira ku san ita ma dominsa ne,
Dukkan halittu ma dominsa ne,
Allah ya yo su ku san ba don mu ba.

Wannan ya sa mu muke bege ga shi,
Har ma muke ta salati kai na shi,
Allah haɗa mu muhalli guda da shi,
Ba can gida na azaba Jahimu ba.

Tammat bi hamdulla mun dakata,
Ɗaliban Lubabatu ne ke ce mata,
Allah ya sa mu cikin Aljannata,
Albarkacin Manzona shugaba.

Waƙar Manzon Allah Rasulullah

Amshi:Manzon Allah Rasulullah,
Begenka muke uban Zara.

Mu wallahi sonka muke,
Manzon kuma duk a gunka muke,
Kullum kuma ƙara sonka muke,
Ka san ba za mu daina ba.

Muna yin gaisuwa gunka,
Muhammadu babu tamkarka,
Domin kuwa duniya donka,
Aka yi ba za mu daina ba.

Wannan waƙa ta Manzo ce,
Muka rera don ko ta dace,

Don murnar samuwatai ce,
Manzonmu Sayyadi babba.

Ya ku jama'a ku saurara,
Mata da maza da 'yan yara,
Ku taho mu riƙe uban Zara,
Sannan mu yawaita yin bauta.

An haifi Rasulu wannan wata,
Na Rabi'ul Auwali ba ɓata,
Ran sha biyu ne wannan wata,
Isinani ba za mu manta ba.

A cikin kuma shekarar giwa,
Abraha ya zo mutum wawa,
Ka'aba wai za ya rushe wa,
Bai san Allah yana nan ba.

Aka yo aike zuwa gun su,
Na tsuntsaye da dutsensu,
Na jahannama don a hore su,
Ba a bar su su kai da bante ba.

Baƙuraishen Hashinmawa ne,
Jikan Abdul Muɗallabi ne,
Ga Abu Ɗalib ko shi ɗa ne,
Ba mu ce ba za mu sanya ba.

Kakanni nasa ma ga su,
Da Kusayyu, Kilabu mun sa su,

Har ma Abdulmanaf ga su,
Ba mu ce ba za mu sanya ba.

Hashim da Kilabu mun sanya,
Mun fatan babu jayayya,
Su Lu'ayyu suna a kan hanya,
Ba mu kasa shigo da su nan ba.

Babarsa ku san Aminatu ce,
'Yar Wahabu ɗiyar mutunci ce,
Nasabar nan tasa ta dace,
Kuma ta isa ai yabo babba.

An haifi Rasulu can Makka,
Birnin mai kyau da albarka,
Allahu ka sa mu je Makka,
Mu gano Ka'aba wuri babba.

A wurin su Larabawan da,
In har an haihu tun can da,
Ƙauye 'ya'yan su kan mai da,
Ba birni za a ƙyale ba.

Sun ce ƙauye akwai iska,
Mai kyau kana da bin doka,
Harshe, ɗa'a da jaruntaka,
Ba za a haɗa da birni ba.

Shi ma Manzo ko an kai shi,
Ƙauye domin a raine shi,

Ya zamanto babu tamkar shi,
Ba a bar shi gida ya zauna ba.

Fa Halimatu Sadiyya babba,
Ita tai rainonsa ba taba,
Ba ta sa ya sha ƙishirwa ba,
Ko yunwa ko tsiraici ba.

Allah ya tashi ikonsa,
Ya aika Mala'iku gunsa,
Su cire nama a ƙirjinsa,
Don tsaftace shugaba babba.

Hadimarsa Halima ta firgice,
Ta tashi ƙwarai ta ɗimauce,
Ta ɗauki Rasulu har ta ce,
Ba za na bari ka zauna ba.

Sai Makka ta mai da shi gu nata,
Babarsa Amina don kanta,
Ta karɓa ta yi murnarta,
Kuma ta yi yabo a kai babba.

Shi Manzo tun yana yaro,
Bai yin cuta ga ko ƙwaro,
Ko shi ɗaya ko cikin taro,
Ba za ka ga ya yi wasa ba.

Ga amana ga riƙon gaskiya,
Shi kun san ba ya yin waskiya,

Kana kuma ba ya yin ƙarya,
Ba za ya faɗi ya canza ba.

Halaye kaf na dattako,
Ya tattara su ya ɗauko,
Jama'arsa sukan yi mamako,
Don halin kamili babba.

A cikin haka har Hadiza ta ji,
Ta kira shi ya je wajenta ta ji,
Ta gwada shi a kan abin da ta ji,
Ta gano bai tsaya nan ba.

Wannan ne ma ya sanya ta,
Neman aurensa don sonta,
Da halayensa sun tabbata,
Ba wanda ake gudu ne ba.

Shiriyar Allah da saƙonsa,
Sun zo hannun Rasulunsa,
Musulunci da ƙa'idojinsa,
Ba a bar shi kawai ya zauna ba.

Aka ce ya kira mu bin Allah,
Mu tsaya daidai a kan sallah,
Azumi, zakkarmu don Allah,
Ba za su bari mu taɓe ba.

In ko muka ce ko ƙarya ne,
Zancen Manzonmu shirme ne,
Muka ɗauka wai mafarki ne,
Allahu ba za ya ƙyale ba.

Nan ga Aljanna can ga wuta,
In kai sharri ka faɗa wuta,
In kai hairi ka kauce mata,
Aljanna kawai guri babba.

Shi ɗan Aljanna ya huta,
Komi ya biɗa a ce kwanta,
Ba ya wahala a sassanta,
Ba za a bari ya koka ba.

Shi ko ɗan wuta ya wulaƙanta,
Don tun nan za ya gigita,
Zai dulmuya can ciki ya ɓata,
Ba za a raga garai sam ba.

Makarantar tamu ta ɗaukaka,
Lubabiyya ga ta ta haskaka,
Allahu ka sa mu bi mai Makka,
Ba bin wani mai gazawa ba.

Tammat mun ƙare waƙarmu,
Da mukai ta yabonsa Manzonmu,
Allah ka ƙaro ilminmu,
Mu tsaya ga Rasuluna babba.

Waƙar Ɗahana Rasulullah

Amshi:Allah abin tsoro,
Ɗahana Rasulullah
La'ilaha illallah,
Muhammadur Rasulullah.

Bege nake kullum,
Ga Ɗahana Rasulullah.

Matuƙar burina,
In gane ka Sallallah.

Don ni a guna ni,
Ba kamar Rasulullah.

Lubabiyya mu ma,
Mun yabon Rasulullah.

Makaranta ce fa,
Ta yabon Habibullah.

Ta cikin New Site,
Jami'ar Rasulullah.

Ɗalibai da malamai,
Na yabon Nabiyullah.

Mun yi salla mun yi yabo,
Ga Rasulu Habibullah.

Zuciyarmu ta yi fari,
Don saboda Rasulullah.

Lahirarsa ta gyaru,
Mabiyinka Sallallah.

Za a ba shi gida mai kyau,
Za ya sami Karamallah.

Ba abin da zai nema,
Ya rasa a gun Allah.

Tanaji na jin daɗi,
Ga maso Rasulullah.

Maƙiyanka Rasulullah,
Sun guje batun Sallah.

Tsabar azaba kaf,
Ga maƙi Rasulullah.

Za ya sha Hamin sosai,
Da zaƙum a gun Allah.

Mun taƙaita yau haka nan,
Kan yabon Rasulullah.

Tammat bi hamdillah,
Godiya wurin Allah.

Waƙar Al'arabiyyul Hashimiyyu Muhammadi

Salamu alaikum jama'a ku mu saurara,
Bagensa nake son zan yi Ɗaha abin ƙauna.

Da farkon salati gaisuwa ga Rasulullah,
Da Alai, Sahabbai, Tabi'ai ga abin ƙauna.

So ya tsawaita nawa gun ka Rasulullah,
Mayafin tunani ya rufe ni abin ƙauna.

Dare da rana gyangyaɗi ko ko a zaune,
Ina tunani Ɗaha shi ne abin sona.

Ka tallafi wannan hadiminka faƙiri ne,
Ka yarda in ganka Sidi ko bayan raina.

Ba ni da kowa Sidi kai ne igiya ta,
Ka yarda da ni sannan ka so ni abin sona.

Kai ne zamana Sidi kai ne tafiyata,
A duk lamarin nan Sidi kai ne muradina.

Kai ne tufata Ɗaha kai ne abincina,
Wallahi Ɗaha, Aminu, kai ne ruwan shana.

Hairatu halƙillahi Ɗaha Muhammadi,
A sammai da ƙassai a ko'ina fa abin ƙauna.

Idanuwa sun ƙagauta da dubawa,
Su gan ka in huta Sidi ko bayan raina.

Komai da komai na bari ga Muhammadi,
Antal Waliyyu na sallama maka duk kaina.

Don na gani mai son ka ya kuɓuce Lazza,
Sidi ka tsere dai da ni fa abin sona.

Mai son ka shi ne ya wadata abin sona,
Mai ƙin ka ni kam ba ni son sa abin ƙauna.

In na jiyo mai ƙin Habibu ina kwance,
Sai hankalina ya tashi don ka abin ƙauna.

Duk maƙiyin Ɗaha, Aminu, abin sona,
Ya tuba ya daina in ko ya ƙi ya bar sona.

Habibi, Shafi'i Sayyadi wa Muhammadi,
Kai man lumana na yi nisa a shauƙina.

Babu mutum ko aljani haka tsuntsaye,
A sammai da ƙassai ba kamarka abin ƙauna.

Babu nabiyyu ba'adahu har can ƙarshe,
Farko da ƙarshe ba kamarka abin ƙauna.

Babu masoyin Ɗaha, Sidi abin sona,
Sai ya rabauta haƙƙu ne iƙrarina.

Ku tashi mu so shi son mu sami rabo babba,
Mu roƙi kusanci gare shi, shi ne muradina.

Wanda yake son Sidi, Ɗaha abin sona,
Ya hau muƙami wanda shi ne tafarkina.

Sai in yi murna mai yawa don mun ƙaru,
Cikin sa masoya gun Habibu abin ƙauna.

Wallahi ni'imaz ziyadu Sidi abin ƙauna,
Masoyanka ne dukkanmu ni da iyalina.

Baiwa ta Ɗaha ta wuce da a ƙirga ta,
Wallahi Allah ta wuce iƙrarina.

Mai kyan wushirya Sidi ga kyan saje,
Kyawonsa Ɗaha ya gajarce misalina.

Ba shi gajeru Ɗaha ba shi ga dogaye,

Ya daidata Sidi ka wuce tsarina.

Ga shi da haske kamar wata na daren sha buɗu,
Don Allah Ɗaha ka haskaka mini ruhina.

In yai tafiya Ɗaha Sidi a kan yashi,
Ba a ganin sawun Habibu abin ƙauna.

Wannan mu'ujiza Sidi ni ta burge ni,
Ka yarda in ganka Ɗaha ko bayan raina.

Amiru bil-ma'arufi, nahi anil – munkar,
Adilu ne Ɗaha, Aminu, abin bina.

Ga haƙuri sannan ko ga shi da jin tausai,
Don tausayinsa ya wuce iƙrarina.

Ya 'yan'uwana me zai hana mui koyi nai,
Mu ƙanƙame sunnar Ɗaha Sidi abin ƙauna.

Yara ƙanana mu sha da su ƙwayar son sa,
Su tashi suna son Ɗaha shi ne abin sona.

Haƙƙin iyaye ne kaza kuma malamai,
Su tashi su dage don su nuna tafarkina.

Wannan nasiha ce gare ku abin bina,
Mu miƙa wuyaye gare shi, shi ne muradina.

To, jama'a horon da nay yi mu gane shi,
Mu tashi mu miƙe gare shi abin sona.

Tammat bisalli alan Nabiyyi Muhammadi,
Da Alai, Sahabbai Auliya'u abin bina.

Fure ne na bege don ku san shi ku gane shi,
Mu dage mu zam koyi da Ɗaha abin ƙauna.

13/03/1414 H.
30/08/1993 M.

Waƙar Rasulu Abin Biya

Da sunanka Rahamanu zan fara waƙa,
Ta begen fiyayye maso gaskiya.

Ina sallama gun ku ya 'yan'uwana,
Da lale ga shumagaban Ambiyya.

Muhammadu ya zo da shirya ga kowa,
Da addin da shar'a ta yin gaskiya.

Musulmi ta bege suke yi ga juna,
Da sumunka shumagban Ambiya.

Cikin shekarar nan ta giwa a Makka,
Wilada ta shumagaban gaskiya.

Mahaifi nasa don mu san shi mu gane,
Ana ce da shi Abdu gwarzo ɗaya.

Da kaka akwai shi ga Manzo mu san,
Fa shi ne Muɗallab maso gaskiya.

Ta Manzo Madina a kai sallama,
Da Hijira, Musulmi su kai tashiya

A nan ne fa addin ya kankama sosai,
Ibada da halin zaman gaskiya.

Musulmi fa sun sami ‘yanci da wala,
Da tsayar da shari’a ta yin gaskiya.

Muna yin ta murna ga mai gaskiya,
Ga Almusɗafa mai dare safiya.

Ina yin salati ga Almusɗafa,
Muhammadu shumagaban gaskiya.

Muna kyauce sunanka ya Rabbana,
Da yab ba mu fursa muna godiya.

Waƙar Rasulullahi Manzon Tsira

Muna murna da Manzonmu Muhammad,
Rasulullahi ya zo ne da tsira.

Da sunan Rabbu kowa ke buƙata,
Ina roƙo ga Allah ban basira.

Na zam kullum yabon Ɗahe Muhammad,
Habibi Musɗafa gwarzo na Zahra.

Da aminci da shirya duk gare shi,
Ga Manzo Murtala ya sami tsira.

Da Alaye, Sahabbai nai jami'an,
Da Tabi'ai da duk mai bi ka ƙara.

Mala'iku a rannan sun yi murna,
Da haihuwa ta Ɗahe sun bishara.

Farin rai kai ya komo duk gare su,
Da yas sauka da sauƙi ba lalura.

Muhammad ya tafo komi da komi,
A cibinai da yanka ba tsirara.

Da jiɗarsa Rasulullahi Manzo,
Gumaka duk na Makka babu tara.

Da ɗai-ɗai sunka reje ba jidali,
Da albarka ta Manzo sun zurara.

Ku san koway yi imani da Allah,
Ya gaggautar da bai'a ba dibara.

Ga Manzo Mujtaba Manzon hidaya,
Rasulullahi mai baiwa kwarara.

Rasulullahi ya zo duk da shirya,
Da *Kur'ani*, Hadisi ba ya jaura.

Da salla har da zakka sa su kono,
Umurni ne na Allah yi da gara.

Da hajji in da iko sa da azmi,
Ibada ce ta farli ban da yara.

Mu zam ilmi mu zam koyi da sunna,

Mu zan wa maluma ɗa'a ta ɗora.

Su ko mata su zam ɗa'arsu gaya,
Ga haƙƙin nan na aure duk su tara.

Su kame ban da wargi ban da wasa,
Su jimre sui biya don ba hasara.

Maza ko sai ku daure kun ga aure,
Tafarki ne na Manzo mai kadaura.

Ina gode wa Allah nan ta ƙare,
Ga waƙar nan ta Manzo mai bushara.

Waƙar Neman Ceton Manzon Allah,
Sallallahu Alaihi wa Sallama

Amshi: Roƙonka muke Rasulinmu,
Manzon Allah buƙata mu,
Cetonka da ke wurin Allah.

Alhamdu mu gode Sarkinmu,
Sarkin ni'ima da yab ba mu,
Komai da a yau muke samu,
Domin Mukhtari Manzonmu,
Uban Rakiya Rasulullah.

Muna roƙonka ya Allah,
Ka daɗo hikimarka ya Allah,
Domin yin ambato Jallah,
A wurin Manzonka ya Allah,
Muhammaduna Rasulullah.

Manzon Allah muna sonka,
Daga zuci ciki muke sonka,
Ya Allah don habibinka,
Sanya son nan ya zarce haka,
A zuƙata don Aminullah.

Ɗan Abdu Balaraben Makka,
Na Amina Rasulu ba shakka,
Kowa ka gani cikin Makka,
Tabbas mun san yana sonka,
Baban Kasim Shafi'ullah.

Sunansa guda Ɗari biyu ne,
Da guda ɗaya mun sani haka ne,
Kirga ka gani ka dai gne,
Domin ka sani sanin zaune,
Sunaye nai Rasulullah.

Muhammadu ne na farkonsu,

Sannan Ahmad yana bin su,
Sai Hamidu ne na ukkunsu,
Fatan da muke fa kun sansu,
Sunaye nai Rasulullah.

Ya tashi yana maraya ne,
Uwa da ubansa kun gane,
Ba ko ɗaya sai mutum biyu ne,
Suka yo rainonsa don su ne,
Dangi a wurin Rasulullah.

Halimatu godiya gunki,
Don ko kin zam macen kirki,
Kowa yau na yabo kanki,
Don ko kin kyauta aikinki,
Rainon Manzo Rasulullah.

Jibrilu ya je ya same shi,
A cikin kogo ya dafa shi,
Saƙon Allah ya kai gun shi,
Yai umurni ya ce tashi,
Yi karatu ya Rasulullah.

Saƙon Allah guda ɗaya ne,
Mu shaida shi fa Allah ne,
Da babu kamarsa shi ɗaya ne,
Muhammadu shi ko Manzo ne,
Na Allah ya Rasulullah.

Mu zam Salla muna Zakka,
Mu je Hajji can zuwa Makka,
Kar mui wasa mu je Makka,

Mai yin wannan fa ba shakka,
Zai sadu da shi Rasulullah.

Tammat mun ƙare waƙarmu,
Da a kai tsari ga yaranmu,
Bisa roƙo nan ga Manzonmu,
Cetonai ya Rasulinmu,
Muhammaduna Nabiyullah.

KAMMALAWA

An rubuta wannan littafi ne don ya yi wa mutane tambihi da tunasarwa da sanar da su wasu matakai na ibada a cikin addinin Musulunci. Ibadar mutum ba ta cika sosai, ballantana Allah ya karɓe ta, sai idan an yi ta bisa ilimi. Wajibi ne ga kowane Musulmi ya bi umurnin Allah da Manzonsa ya tashi tsaye, tsayin daka, ya nemi ilimin sanin Ubangijinsa da na hanyoyin yi masa bauta da na hulɗa da sauran 'yan'uwansa, 'yan'adam.

A littafin an nemi dukkan mutane da su yi imani da Allah, su kaɗaita wahadaniyarsa, su zamanto masu sakankancewa zuwa gare shi. Allah shi ne mahaliccin komi da kowa, shi ne ya yi mutane da dabbobi da itatuwa da tsirrai da sammai da ƙassai da kowace irin halitta wadda za a iya tunanowa da wadda ba a san ta sam ba.

Haka kuma an bayyana wajibi ne mutum da aljan su yi wa Allah ibada, ba tare da yin shirka ba. Ibadar nan kuwa ta ƙunshi bin abin da Allah ya yi umurni da a yi, da barin abin da ya yi hani a kansa, sannan da ƙoƙarin kyautatawa a cikin ayyukan ibada da hulɗa ko ma'amala da sauran dangogin mutane.

Har wa yau, an nuna wanda ya yi ƙoƙarin kiyaye kansa kuma ya daidaitu bisa aikin ibada, shi ne zai sami rabo babba, Allah kuma ya yi masa sakamako da rahamarsa da jinƙansa. Allah ya bayyana ta hanyar Manzanninsa matsayin shari'arsa da addininsa na Musulunci. Ta haka ne aka san Musulunci an gina shi ne a bisa abubuwa guda biyar wato gaskata Allah da Manzonsa da Salla da Zakka da Azumi da Hajji. Bayan waɗannan muhimman turakun addinin Musulunci da aka yi wa Musulmi baiwa da su, an kuma dabaibaye dukkan rayuwarsa ta yau da kullum da bin tafarkin Musulunci. A

wajen aure ne ko haihuwa ko mutuwa ko neman ilimi ko aiki da shugabanci ko kasuwanci ko ciniki da saye da sayarwa ko a farke ne ko ana bacci, ko ana wani aki ko ba yi da sauransu duk an nemi a yi su bisa kyautace niyya da bin shari'a.

Kuma an zo da bayanai da suka shafi hukunce-hukuncen ibada kan waɗannan abubuwan da aka zayyana a baya kaɗan, tun daga kalmar shahada wato tauhidi ko kaɗaita Allah da salla da zakka da azumi da hajji da sauran ayyukan rayuwar ɗan'adam.

A littafin, har wa yau, an yi bayanin yadda Allah ya halicci ɗan'adam bisa zaɓinsa (Allah), ya neme shi ya yi bauta, sannan aka aiko Annabawa da Manzanni don su yi jagora wajen fahimtar da yadda za a yi wa Allah bauta. Bayan an gabatar da wannan zance, sai aka zo da wasu ɓangarori da suka danganci sirar Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, tun daga haihuwarsa da ƙuruciyarsa da halayensa da aiko shi da aka yi a matsayin Annabi kuma Manzo da bayanin zuriyyarsa da alayensa da sauran danginsa da Manzancinsa da abubuwan da ya zo wa duniya da su sababbi.

Har wa yau, a wannan littafi an kawo wasu waƙoƙi rubutattu da aka rubuta su don su koyar da ilmin yi wa Allah ibada. Bayansu kuma an shimfiɗa wasu waƙoƙi waɗanda suka ƙunshi matani na yabo da bege ga Manzon Allah, Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su tabata a gare shi.

Wajibi ne gare mu Musulmi mu tashi, mu dage wajen yi wa Allah bauta, kuma mu nemi ilmin yin haka. Allah ya ce:

> "Allah (shi kaɗai ne) babu wani abin bautawa da gaskiya sai shi. Rayayye, mai tsayuwa (da shirya al'amuran talikai). Ya saukar da littafi a gare ka da gaskiya (yana) mai gaskatawar abin da yake gabaninsa (na littattafai), ya kuma

saukar da *Attaura* da *Linjila*. (Ya saukar da su) tuntuni don shiriya ga mutane, ya kuma saukar da littattafai masu rarrabewa (tsakanin gaskiya da ƙarya). Allah kuwa mabuwayi ne, ma'abocin azaba mai tsanani (ga waɗanda suka kafirce masa)" (Ali Imrana, aya ta 2 – 4).

A wata aya kuma Allah ya ce:

"Ya Ubangijinmu! Kada ka karkatar da zukatanmu bayan har ka shiryar da mu, kuma ka ba mu rahama daga gunka. Lalle ne, kai, kai ne mai yawan kyauta. Ya Ubangijinmu! Lalle ne, kai, mai tara mutane ne domin wani yini wanda babu shakka a gare shi. Lalle ne Allah ba ya saɓawar lokacin alƙawari" (Ali Imrana, aya ta 9 – 10).

Muna yi wa Allah godiya da ya yi mana baiwa da karimci bisa samun Annabi Muhammadu, tsira da amincin Allah su ƙara barbazuwa zuwa gare shi da Alayensa da Sahabbansa da duk wanda ya bi su da shiriya har zuwa Lahira. Allah abin godewa ne kuma bisa ɗaukakar da ya yi mana da samun hasken Musulunci mai miƙaƙƙen godabe, tsayayye. Ya Ubangijinmu, Allah ka yi mana luɗufi, ka karɓi ibadarmu ba don halinmu ko ayyukanmu ba.

Muna roƙon Allah ya yi mana fatahi da albarkar *Alƙur'ani*, ya azurta mu da albarkar bin umurninsa da guje wa haninsa. Muna kuma roƙon Allah ya ba mu falalar hadisan Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, da abin da malamanmu masu girma suka haɗu a kansa.

Allah ka yi gafara a gare mu, da iyayenmu maza, da iyayenmu mata, da muminai, maza da mata da sauran jama'ar Musulmi, mazansu da matansu. Allah ka shiryar da mu, ka shiryar da 'ya'yanmu, da dukkan waɗanda suke a bayanmu. Sannan ka 'yanta iyayenmu daga shiga wuta, da iyayen iyayenmu, maza da mata. Allah ka yi mana gamon katar da Aljannarka mai ni'ima, ka sadar da mu a ko da yaushe da mutanenka na ƙwarƙwarai, masu jinƙai da tausayi na ƙasa da su. Allah ka kiyaye mu daga faɗa wa cikin ayyukan saɓonka, ka jefa tsoronka a cikin zukatanmu, ka sanya babbar garkuwa a tsakaninmu da hanyoyin ƙin bin umurninka. Ka ba mu ikon yi maka ɗa'a wadda za ta yi mana jagora zuwa Aljannarka, ka tunkuɗe mana musibun da ke yawo a duniya.

Allah ka jiyar da mu dadi da sunayenmu da gannenmu da ƙarfinmu, tsawon kwanukan da ka rayar da mu, ka sanya shi gado a tsakaninmu. Allah ka ɗaukar mana fansa ga wanda ya zalunce mu, ka yi mana taimako a kan wanda yake cutar da mu, kada ka sanya wata fitina ko musiba a addininmu, Allah kada ka sanya son duniya, ya zama shi ne abin fifitawarmu, ko ma'isar ilminmu, kada kuma ka ɗora mana shugaban da ba zai yi mana rahama ba, ya mafificin mai yin rahama, ya Ubangijin talikai.

Allah ka yi tsira ga Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, wanda hasken halittarsa ya riga dukkan sauran halittu, bayyanarsa ta zama rahama da jinƙai ga 'yan'adam (halittu). Ka yi tsira ya Allahu gare shi kwatankwacin yawan waɗanda suka shuɗe na halittunka, da gwargwadon waɗanda suka rage, tsira da ba ta da iyaka ba ta da ƙarshe, kuma ba ta tsinkewa, tsira wadda take dauwamammiya da dauwamarka.

Allah ka biya mana dukkan bukatunmu da albarkar Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama, ka

tsarkake mu daga dukkan zunubai, ka tsare mu daga abubuwan tsoro, ka ɗaukaka darajarmu a wajenka, ka ba mu dukkan alheranka a wannan rayuwa ta duniya, da bayan mun fadì mun rasu.

Allahumma salli wa sallim ala Sayyadina Muhammadin wa ala Alihi wa Sahbihi wa sallama Taslima. Walhamdu Lillahi Rabbil Alamina.

MANAZARTA

Alƙur'ani, mai Tsarki.

Al'akhdari, S. A. (Babu Shekarar Bugawa). *Mukhtasarul Akhdari.* Kano: Alhaji Ahmad Tijjani ya Buga.

Alƙayyim, A. (1401 H.). *Sifatil Munafiƙina.* Babu Sunan Maɗaba'a.

Assa'adi, A. N. (1409 H.) *Alwasa'ilil Mustafidati Lihayatis Sa'idatu.* Riyad, Saudiyya: Al'idaratil Ammati Liɗɗab'i Wattarjamati.

Babu Sunan Mawallafi. (Babu Shekarar Bugawa). *Al'aƙaidu Attauhidiyya.* Beirut: Dar Alfikri.

Babu Sunan Mawallafi. (Babu Shekarar Bugawa). *Siratu Annabiyi, Sallallahu Alaihi Wasallam.* Kano: Alhaji Sharif Sanusi ya Buga.

Basɗi, M.A. A. (1321 H.) *Hayatul Islam.* Kano: Alhaji Sharif Bala Gabari ya Buga.

Baz, A. A. (1990). Wujubul-Amali bi Sunnatil-Rasuli, *Sallallahu Alaihi wa Sallama wa Kufri man Ankaraha.* Riyad, Saudiyya: Al-Idaratil Ammati Liɗɗb'i wal Tarjamati.

Clarke, P. B. (1982). *West Africa and Islam.* London: Edward Arnold Publishers Limited.

Ɗanfodiyo S. U. (Babu Shekarar Bugawa). *Kitabu Usuluddini.* Zaria: Gaskiya Corporation.

Ɗanfodiyo, S. U. (1993). *Wasiƙa zuwa ga 'Yan'uwa.* Fassarawar Hajiya Gambo Umaru Jikan Dabo Tsiga. Malumfashi: Lamp, 36 Maude Road.

Fodiyo, A. (Babu Shekarar Bugawa). *Tahzibul Insan.* Lagos: Attauheed Publishing Company.

Gummi, A. M. (1979). *Alƙur'ani mai Girma da Kuma Tarjamar Ma'anoninsa zuwa ga Harshen Hausa.* Riyad, Saudiyya: Wikalatu Shu'uni Almaɗbu'ati wa Annashri.

Gummi, A. M. (Fassara) (Babu Shekarar Bugawa). *Matanul Arba'in Annawawiyya.* Beirut, Lebanon: Dar Al'arbiyya.
Gusau, S. M. (1994). *Mu Koyi Ibada.* Kano: Gidan Dabino Publishers.
Gusau, S. M. (1991&2005). *Musulunci da Bazuwarsa.* Kano: Benchmark Publishers Limited.
Gusau, S.M. (1991&2005). *Mazhabobi Huɗu da Yaɗuwarsu*. Kano: Benchmark Publishers Limited.
Gusau, S.M. (1991&2005). *Shari'a a Musulunci*. Kano: Benchmark Publishers Limited.
Hussaini, H. M. (Babu Shekarar Bugawa). *Ta'alimiddini wa Arkanul-Islam.* Beirut, Lebanon: Almaktabatu As-Sha'abiyya.
Iman, A. A. (1970&1975). *Tarihin Annabi Kammalalle.* Zaria: NNPC.
Isik, H. H. (Babu Shekarar Bugawa). *Belief in Islam.* Turkey: Isik Kitabari Darussaƙafa Gaddesi No. 72.
Islamiyyatu, Aljamhuriyyatu. (1993). *Kira'atun fi Al-Nafsi al-Insaniyyati.* Iran: Lajnati Atta'arif wa Mu'assassatu Albalag.
Islamiyyatu, Aljamhuyiyyati. (1993). *Haƙƙu Zawil- Kurba.* Iran: Lajnatu Ata'arif wa Mu'assasatu Algalag.
Maijega, M. B. (1990). *Tarihin Masallaci a Musulunci.* Kaduna: Fisbas Media Serɓices.
Musɗafa, S. N., Sa'id, B., Yusuf, A. T. (1993 M. / 1413 H.). *Tataccen Bayani na Ma'anonin Alƙur'ani.* Kano, Nijeriya: Maɗaba'ar Mainasara.
Ri'asatil Ammati. (1991) *Albayanul Mufid.* Riyad, Saudiyya: Al'idaratil Ammati Liɗɗab'i wattarjamati.
Rufa'i, M. K. (1976). *Aƙidatul Muslim Minal Kitabi was Sunnati.* Cairo: Darul I'itisam.

Sadiƙ, M. A. (Babu Shekarar Bugawa). *A Guide to Prayer in Islam*. Babu Sunan Maɗaba'a.
Wali, N. S. (Babu Shekarar Bugawa). *Giza'ul Wildani fi Aƙa'idil Iman.* Cairo: Maɗaba'ati Mashhadi.

RATAYE

JERIN WASU TAMBAYOYI

An shirya waɗannan tambayoyi ne don su taimaka wa malamai da ɗalibai da sauran jama'ar Musulmi don su yi wa kansu tambihi ta bincika harkokinsu na sha'anin addininsu. Har wa yau kuma za su taimaka wa mutum ya dinga yi wa kansa hisabi tun kafin ya sami kansa a wajen hisabi na Lahira. An shirya tambayoyin ne ta yadda za a iya samun amsoshinsu idan aka koma cikin wannan littafi a sauƙaƙe. Yi wa kanka hisabi kana yi kana mai konkomawa tun kafin a yi maka. Ga tambayoyin kamar haka:

Mene ne addinin Musulunci?
Mene ne Imani? Mene ne alamomin imani?
Rukunan Imani guda nawa ne?
Ta yaya za ka iya bayyana hanyoyin Ihsani?
Wace hanya ce za a iya gane Allah?
Siffofin Allah guda nawa ne?
Kawo siffofin Allah wajibai?
Kawo siffofin Allah korarru?
Wace irin siffa ce take zama ja'iza ga Allah?
Bisa waɗanne irin abubuwa ne aka gina Musulunci?
Mece ce ibada?
Mece ce bauta?
Wane ne ya cancanci a yi wa bauta?
Don me Ubangiji ya halicci mutum da aljan?
Mene ne matsayin mutum a wajen ibada?
Bayyana dangogin tsarki.
Bayyana alwala da yadda ake yin ta?
Salloli na farilla guda nawa ne?

Salloli na nafila nau'i nawa ne?
Waɗanne lokatai ne na salla?
Mece salla?
Ta yaya ake shirya wa yin salla?
Faɗi yadda siffar salla take?
Wane irin wuri ake so a yi salla a kansa ko a cikinsa?
Wane mutum ne salla ta wajaba a gare shi?
Mene ne hukuncin wanda ya ƙi yin salla?
Bayyana adadin salloli na nafila da ake yi a daura da salloli na farilla kafinsu da bayansu?
Bayyana raka'o'in salloli na farilla?
Bayyana farillan salla da sunnoninta da mustahabbanta?
Waɗanne irin abubuwa ne ke ɓata salla? Lisafa su daki-daki?
Mene ne ba'adi ko ƙabli?
Yaya ake yin ba'adi? Bayyana wuraren yin ta?
Yaya ake yin ƙabli? Bayyana wuraren yin ta?
Ko akwai raukanuwar da ba ta sa ba'adi ko ƙabli?
Mene ne azumi?
Su wane ne aka rangwanta wa yin azumi?
Yaya ake yin azumi?
Bayyana farillan azumi da sunnoninsa?
Waɗanne irin abubuwa ne ake so ga mai azumi ya aikata?
Mene ne Hajji?
A wace shekara aka wajabta Hajji?
Bayyana rukunan Hajji da farillansa da sunnoninsa?
Mene ne ake so mahajjaci ya aikata?
Mece ce Zakka?
Mene ne matsayin Zakka a Musulunci?
Waɗanne irin abubuwa ne ake yi wa Zakka?
Farillan Zakka nawa ne? faɗe su?
Bayyana ladubban Zakka?
Su wane ne ake ba Zakka?

Mene ne maganin cutar zunubai?
Wace irin wasiyya ce Ubangiji ya yi wa Manzonsa?
Waɗanne halaye ne guda biyu ake so a yi riƙo da su?
Waɗanne ayyukan alheri ne aka yi kwaɗaitarwa a kansu?
Bayyana yadda za a baza himma a cikin ibada?
Waɗanne ne musibu uku na ƙarshen duniya?
Mene ne sakamakon wulaƙanta abubuwa biyar?
Su wane ne mutanen ƙwarai?
Su wane ne ashararai?
Mene ne matsayin mace mai haila?
Mene ne matsayin mace bisa umurnin mijinta?
Mene ne sakamakon mace idan ba ta yi wa mijinta kyautatawa ba?
Ko ana son mace ta ɗora wa mijinta ya yi mata abin da ba zai iya yi ba?
Mene ne sakamakon miji wanda yake barin matarsa ta sanya turare idan za ta je unguwa?
Ko mace na iya fita daga ɗakinta ba tare da izinin mijinta ba?
Mane ne sakamakon mata mai kyautatawa mijinta?
Akwai wasu mata da Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya gani a lokacin Isra'i da Mi'iraji, su wane ne waɗannan mata? Faɗi sakamakon da suka samu saboda ayyukansu?
Waɗanne mutane ne guda huɗu Allah ya kafa hujja da su?
Bayyana ma'anar Ranar Ƙarshe da Ranar Tashin Kiyama?
Bayyana alamomin Tashin Ƙiyama?
Wane ne mutum?
Bayyana yadda aka yi halittar mutum?
Mene ne bambancin Annabi Adamu da Annabi Isa a wajen halittawa?
Wane ne ake ce wa Annabi?
Wane ne Manzo?

Mene ne bambanci tsakanin Annabi da Manzo?
Annabawan Allah guda nawa ne?
Manzannin Allah guda nawa ne?
Wane Annabi ne aka fara aikowa?
Wane ne kuma ya zama Annabin ƙarshe?
Wane ne Annabi Muhammadu, sallallahu alaihi wa sallama?
Bayyana gari da ƙabilarsa?
Mece ce nasabar Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama?
Zayyana wasu daga cikin halayen Manzon Allah.
Fadi wasu daga cikin ɗabi'unsa.
Waɗanne abubuwa ne Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya zo da su?
Matan aure guda nawa ne Manzon Allah ya aura? Fadi sunayensu?
Waɗanne irin abubuwa ne Manzon Allah ya keɓanta da su?
Fadi wasu daga cikin mu'ujizojin Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama.
Ayyana fasahar harshen Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama?
Fadi wasu daga cikin maganganun fasaharsa, sallallahu alaihi wa sallama.
Yaushe ne Manzon allah, sallallahu alaihi wa sallama, ya yi wafati?
Mene ne amfanin waƙa ga mutum?
Fadi kanun wasu waƙoƙin da aka rubuta don koyar da ibada?
Fadi sunayen wasu waƙoƙin yabon Manzon Allah, sallallahu alaihi wa sallama?
Me ake nufi da begen Manzon Allah?
Me ake nufi da yabon Manzon Allah?

Adabin Hausa

1. **Wasanni Don Yara, 1982, Ganuwa Publishers, Zaria.**
2. **Darussan Hausa I,II,III (Ha]in Guiwa), 1992 & 1993 UPL, Ibadan**
3. **Dabarun Nazarin Adabin Hausa, 1995 & 2008, Benchmark Publishers Limited, Kano.**
4. **Maka]a da Mawa}an Hausa, 1996 & 2005 Benchmark Publishers Limited, Kano.**
5. **Tatsuniyoyi a Rubuce, 2000, Gidan Dabino Publishers, Kano.**
6. **Salihu Janki]i SarkinTaushi, 2002, Baraka Press & Publishing, Kaduna.**
7. **Jagoran Nazarin Wa}ar Baka, 2003, Benchmark Publishers Limited, Kano.**
8. **Wa}o}in Baka a {asar Hausa, 2008, Benchmark Publishers Limited, Kano.**

Tarihi

9. **Gusau ta Malam Sambo, 1979. Ganuwa Publishers, Zaria.**
10. **A Short History of Gusau, 1984, Sidi Umar Press, Sokoto.**
11. **Asalin Sarautar [anmasani da Tarihin [anmasanin Gusau, 1992, Abioye Dynamic Printers, Kano.**
12. **Sarautar Matawalle da Tarihin Matawallen Gusau, 1992, Zed Press, Kano.**
13. **Kadaura [an Sulaiman, 1993, Fisbas Media Serɓices, Kaduna.**

Addinin Musulunci

14. **Musulunci da Bazuwarsa, 1991/2005, Benchmark Publishers Limited, Kano.**
15. **Shari'a a Musulunci, 1991/2005, Benchmark Publishers Limited, Kano.**
16. **Mazhabobi Hu]u da Ya]uwarsu, 1991/2005, Benchmark Publishers Ltd, Kano.**
17. **Mu Koyi Ibada I, 1994, Gidan Dabino Publishers, Kano.**

Fassara

18. **Jaririya Mai Al'ajabi, 1998, Cambridge Uniɓersity Press, London.**
19. **Tanko Arausaya, 1998, Cambridge Uniɓersity Press, London.**
20. **Siddabarun Hawainiya, 1998 Cambridge Uniɓersity Press, London.**
21. **Ziyarar Dora, 1998, Cambridge Uniɓersity Press, London.**

Wasu Littattafansa da ke Jiran Bugawa

22. **Wasanni da Wa}e-Wa}en Yara a {asar Gusau, 1980.**
23. **Rayuwa da Ayyukan Mai Martaba Sarkin Musulmi, Alhaji Dr. Ibrahim Dasu}i, 1990.**
24. **Tsokaci a kan Wa}ar Sahibi, 1991.**
25. **Jirwayen Wa}o}in Baka a Harshe da Adabi, 1993.**
26. **Shuni Gyara Zare: Tarihin Rayuwar Alhaji Ladan Abdullahi Shuni, 1993.**
27. **Alhaji Ladan Shuni: The [anmasani of Sokoto, 1993.**
28. **Biyar ta Gusau, 1994.**
29. **Hanyar Nazarin Adabi a Sau}a}e, 1998.**
30. **Hajji da Umra a Sau}a}e, 2002.**
31. **The Mai Bade, Alhaji Umar Sulaiman (English Ɓersion), 2006.**

Mu}alu da Takardu

Farfesa Sa'idu Muhammad Gusau, ya rubuta mu}alu da takardun ilimi da yawa fiye da arba'in da biyar.